



# Suratul Fatiha

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Fuskantar Allah gaba xaya da cikakkiyar bauta gare shi, shi kaxai.**

## Tafsiri:

**An ambaci wannan sura da (Suratul Fatiha) saboda an buxe littafin Allah da ita. Kuma ana kiranta da (Ummul Qur'an) saboda ta tattaro dukkan abubuwan da Alqur'ani ya yi magana a kansu, na daga kaxaita Allah (Tauhidi), da al'amuran ibada, da qissoshin waxanda suka gabata, da sauransu.**

**Ita ce surar da ta fi kowacce sura girma a cikin Alqur'ani, kuma ita ce ake kira da (Assab'ul Masaani) wato ayoyi bakwai da ake yawan maimaita karatunsu.**

**1 Da sunan Allah nake fara karatun Alqur'ani, ina mai neman taimakonsa, mai neman albarka da ambaton sunansa. Bismillah ta kunshi sunayen Allah guda uku, su ne: na farko Allahu wanda yake nufin abin bauta na gaskiya da cancanta. Sannan kuma kevantaccen suna ne na Allah, ba a kiran wani da shi. Na biyu: Arrahmanu: Yana nufin ma'abocin rahama yalwatacciya, don haka shi mai Rahama ne a karan-kansa. Na Uku: Arraahim, wanda yana nufin ma'abocin rahamar da take saduwa da bayinsa, yana jin qan wanda ya so daga cikin bayinsa muminai.**

**2 Dukkan Siffofin yabo da xaukaka da kamala na Allah ne shi kaxai, domin shi ne Ubangijin dukkan komai, kuma mahaliccinsa, mai juya shi.**

**Lafazin (Alaamun) jam'i ne na (Aalam) wanda yake nufin dukkan waxanda ba Allah Madaukakin Sarki ba.**

**3 Wannan yabo ne ga Allah bayan gode masa da aka yi a ayoyin da suka gabata.**

**4 Wannan yabo ne ga Allah cewa shi ne ya mallaki dukkan abin da yake a ranar Alkiyama, ba wata rai da ta mallaki wani abu. (Yaumud Deen) ita ce ranar hisabi da sakamako.**

**5 Muna keve ka kai kaxai da dukkan nau'ikan bauta da biyayya, ba ma haxa wani da kai, kuma gare ka, kai kaxai muke neman taimako a cikin dukkan al'amuranmu, alheri gabaxaya yana hannunka, babu wani mai taimako sai kai kaxai.**

**6 Ka nuna mana tafarki madaidaici, kuma ka xora mu a kai, ka tabbatar da mu a kai, ka qara mana shiriya. Lafazin (Assiraax Al-mustaqeem) yana nufin hanya miqaqqiya, wadda babu wata karkacewa a tare da ita, ita ce musuluncin da Allah ya aiko Manzon Allah Muhammad (S.A.W) da shi.**

**7 Tafarkin waxanka ka yi musu ni'imar shiriya daga cikin bayinka, kamar Annabawa da Siddiqai da Shahidai da nagartattun bayi, Madallah da wadannan abokan zama. Ba hanyar waxanda ka yi fushi da su ba, su ne waxanda suka san gaskiya, amma ba su bi ta ba, kamar Yahudawa. Kuma ba hanyar waxanda suka bace daga hanya ta gaskiya ba, ba su gane ta ba, saboda sakacinsu wajen neman gaskiya da shiriya zuwa gare ta, kamar Nasara ( Wato kiristoci).**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Allah ya buxe littafinsa da Bismillah, don ya nuna wa bayinsa su fara dukkan ayyukansu da maganganunsu da ita, don neman taimakonsa da dacewarsa. 2 - Yana daga cikin shiriyar bayin Allah Salihai a wajen addu'a farawa da yabon Allah da yi masa kirari, sannan sai a fara rokon abin da ake so. 3 - Tsoratar da musulmi da jan kunnensu a kan yin sakaci wajen neman gaskiya, kamar yadda Nasara (kiristoci) vatattu suka yi, ko rashin aiki da gaskiyar da suka sani, kamar yadda Yahudu waxanda aka yi fushi da su suka yi. 4 - Surar ta nuna cewa cikar imani shi ne tsarkake bauta ga Allah da neman taimako a wajensa shi kaxai.**

# Suratul Baqara

An Saukar Da Ita A Madinah

سُورَةُ البَقَرَةِ

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الٓمٓ ١ ذَٰلِكَ ٱلۡكِتَٰبُ لَا رَيۡبَۛ فِيهِۛ هُدٗى
لِّلۡمُتَّقِينَ ٢ ٱلَّذِينَ يُؤۡمِنُونَ بِٱلۡغَيۡبِ وَيُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ
وَمِمَّا رَزَقۡنَٰهُمۡ يُنفِقُونَ ٣ وَٱلَّذِينَ يُؤۡمِنُونَ بِمَآ أُنزِلَ
إِلَيۡكَ وَمَآ أُنزِلَ مِن قَبۡلِكَ وَبِٱلۡأٓخِرَةِ هُمۡ يُوقِنُونَ ٤
أُوْلَٰٓئِكَ عَلَىٰ هُدٗى مِّن رَّبِّهِمۡۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ
هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ٥



## Daga Manufofin Surar:

**Tanadar al'umma don raya bayan qasa, da tsayar da addinin Allah, da bayanin kashe-kashen mutane. Sannan a cikinta akwai bayanin rukunanan addini da abin da shari'ar musulunci ta kunsa.**

## Tafsiri:

**An kira surar da (suratul Baqara) saboda labarin saniyar bani-Isra'ila da ya zo a cikinta. A cikin wannan qissa Allah ya yi nuni zuwa ga gaggawar aikata shari'ar Allah, ba tare da jinkiri ba, kamar yadda Yahudawa suka aikata.**

**(1) Waxannan haruffa suna cikin haruffan da aka buxe farkon wasu surorin Alqur'ani da su. Suna cikin haruffan larabci, kuma ba su da ma'ana idan suka zo su kaxai, kamar a ce (Alifun, Ba'un, Ta'un…) ne, amma akwai hikima da dalilin da ya sa aka ambace su a haka a cikin Alqur'ani, saboda babu abin da ba hikima a cikinsa a cikin Alqur'ani. Babbar hikimar ambatonsu ita ce, yin qalu-bale da Alqur'ani, wanda aka haxa shi da waxannan haruffa da suka sani, kuma suke magana da su (amma sun gagara kawo irinsa). Wannan ya sa sau da dama idan aka kawo su, sai ambaton Alqur'ani ya biyo baya, kamar yadda yake a wannan surar.**

**(2) Wannan Alqurani mai girma babu shakka a cikinsa, ta kowane vangare, vangaren saukar da shi ne, ko vangaren lafazinsa da ma'anarsa. Zancen Allah ne, yana shiryar da masu tsoron Allah zuwa hanyar da za ta sada su da shi.**

**(3) (4) Waxanda suke imani da gaibu. Gaibu shi ne abin da ba ma gani, kuma ba ma iya gane shi da ji, ko gani, ko tavawa, ko shaqa, ko xanxano, daga cikin irin abubuwan da Allah ya bamu labarinsu, ko Manzonsa ya bamu labari, kamar ranar alqiyama.**

**Su ne waxanda suke tsayar da sallah, ta hanyar yin ta kamar yadda Allah ya shar'anta, da sharuxxanta, da rukunanta, da wajibanta, da sunnoninta. Kuma su ne waxanda suke ciyarwa daga abin da Allah ya azurta su, ta hanyar bayar da abin da ya wajaba a kansu, kamar zakkah, ko abin da bai wajaba ba, kamar sadaka, don neman lada a wurin Allah.**

**Su ne waxanda suke imani da wahayin da aka saukar maka, da wanda aka saukar wa da sauran annabawan da suke gabaninka, ba tare da wani bambancewa ba. Kuma su ne suke imani da ranar lahira da abin da yake cikinta na lada ko uquba, imani yankakke wanda babu shakka a cikinsa.**

**(5) Masu waxannan siffofi sune waxanda suke kan tafarkin shiriya, su ne masu rabauta duniya da lahira, ta hanyar samun abin da suke fata, da kuma kuvuta daga abin da suke tsoro.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yankewa da tabbatar da babu shakka a cikinsa (Wato Alqur'ani) dalili ne da yake nuna cewa daga wajen Allah ya ke, saboda babu wani mahalukin da zai yi da'awar haka a kan zancensa, ya ce babu shakka a cikinsa.**

**2 - Babu waxanda suke amfanuwa da manya-manyar shiriyoyin Alqur'ani mai girma sai masu tsoron Allah, waxanda suke girmama shi. 3 - Daga manya-manyan matakan imani, akwai imani da gaibu, saboda ya qunshi sallamawa Allah gabaxaya cikin abin da ya kaxaita da saninsa na gaibu, da kuma sallamawa Manzonsa cikin abin da ya ba da labari dangane da Allah. 4 - Sau da dama Allah ya kan haxa tsakanin sallah da zakkah. Saboda sallah tsarkake zuciya ce ga abin bautawa (Allah), ita kuma zakkah kyautatawa bayi ne. waxannan abubuwa biyu kuma su ne dalilin samun arziqi da tsira. 5 - Yin imani da Allah da aiyuka nagari suna gadar wa mai yin su shiriya da dacewa a duniya, da tsira da rabauta a lahira.**

إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ سَوَآءٌ عَلَيۡهِمۡ ءَأَنذَرۡتَهُمۡ أَمۡ لَمۡ تُنذِرۡهُمۡ
لَا يُؤۡمِنُونَ ٦ خَتَمَ ٱللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ وَعَلَىٰ سَمۡعِهِمۡۖ وَعَلَىٰٓ
أَبۡصَٰرِهِمۡ غِشَٰوَةٞۖ وَلَهُمۡ عَذَابٌ عَظِيمٞ ٧ وَمِنَ ٱلنَّاسِ
مَن يَقُولُ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَبِٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَمَا هُم بِمُؤۡمِنِينَ ٨
يُخَٰدِعُونَ ٱللَّهَ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَمَا يَخۡدَعُونَ إِلَّآ أَنفُسَهُمۡ
وَمَا يَشۡعُرُونَ ٩ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٞ فَزَادَهُمُ ٱللَّهُ مَرَضٗاۖ
وَلَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمُۢ بِمَا كَانُواْ يَكۡذِبُونَ ١٠ وَإِذَا قِيلَ لَهُمۡ
لَا تُفۡسِدُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ قَالُوٓاْ إِنَّمَا نَحۡنُ مُصۡلِحُونَ ١١ أَلَآ إِنَّهُمۡ
هُمُ ٱلۡمُفۡسِدُونَ وَلَٰكِن لَّا يَشۡعُرُونَ ١٢ وَإِذَا قِيلَ لَهُمۡ
ءَامِنُواْ كَمَآ ءَامَنَ ٱلنَّاسُ قَالُوٓاْ أَنُؤۡمِنُ كَمَآ ءَامَنَ ٱلسُّفَهَآءُۗ
أَلَآ إِنَّهُمۡ هُمُ ٱلسُّفَهَآءُ وَلَٰكِن لَّا يَعۡلَمُونَ ١٣ وَإِذَا لَقُواْ
ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ قَالُوٓاْ ءَامَنَّا وَإِذَا خَلَوۡاْ إِلَىٰ شَيَٰطِينِهِمۡ قَالُوٓاْ إِنَّا
مَعَكُمۡ إِنَّمَا نَحۡنُ مُسۡتَهۡزِءُونَ ١٤ ٱللَّهُ يَسۡتَهۡزِئُ بِهِمۡ وَيَمُدُّهُمۡ
فِي طُغۡيَٰنِهِمۡ يَعۡمَهُونَ ١٥ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ ٱشۡتَرَوُاْ ٱلضَّلَٰلَةَ
بِٱلۡهُدَىٰ فَمَا رَبِحَت تِّجَٰرَتُهُمۡ وَمَا كَانُواْ مُهۡتَدِينَ ١٦



**Yayin da Allah ya bayyana siffofin Muminai masu jin tsoronsa, waxanda suka gyara zahirinsu da baxininsu, sai ya ambaci siffofin kafirai, waxanda zahirinsu da baxininsu duk a vace yake, Ya ce,:**

**6 Waxanda suka kafirta sun zarce a kan vatansu da taurin kansu, don haka gargaxinka gare su da babu duk xaya.**

**7 Saboda Allah ya rufe zukatansu, ya kulle su da abin da yake cikinsu na varna, ya rufe jin su, ba sa jin gaskiya, ji na karva da miqa wuya, ya sanya marufi akan idanuwansu, ba sa ganin gaskiya duk da bayyanarta, suna da azaba mai girma a lahira.**

**Bayan Allah ya bayyana siffofin Kafirai, waxanda zahirinsu da baxininsu duka a lalace yake, sai ya bayyana siffofin Munafikai, waxanda baxininsu a vace yake, amma zahirinsu a gyare yake, kamar yadda suke nunawa mutane. Ya ce,:**

**8 Daga cikin mutane akwai wasu jama'a da suke cewa su muminai ne, suna faxa da bakinsu, saboda suna tsoron a zubar da jininsu a tava dukiyarsu, amma fa a voye su kafirai ne.**

**9 Suna yaudarar Allah da muminai ta hanyar bayyana imani da voye kafirci, amma alal-haqiqa kansu kaxai suke yaudara, saboda Allah ya san abin da yake sarari da abin da yake voye, amma su ba sa jin haka, don haka Allah ya bayyana wa muminai siffofinsu da halayensu.**

**10 Dalilin da ya sa suke haka, a cikin zukatansu akwai shakka, sai Allah ya qara musu shakka akan shakkarsu, saboda abin da ka yi shi za a yi maka, kuma suna da azaba mai raxaxi a can qasan wuta, saboda qaryar da suka yi wa Allah da Mutane, da kuma qaryata abin da Annabi Muhammad (S.A.W) ya zo da shi.**

**11 Idan aka hana su varna a bayan qasa ta hanyar aikata kafirci da zunubai da sauransu, sai su yi musu, su ce, su mutane ne nagari masu gyara.**

**12 Amma gaskiyar lamari su mavarnata ne, sai dai ba sa jin hakan a tare da su, kuma ba sa jin aikinsu varna ce tsantsa.**

**13 Idan aka umarce su da imani, kamar yadda Sahabban Annabi Muhammad (S.A.W) suka yi imani, sai su yi musu, su yi izgili, su ce, za mu yi imani kamar yadda mahaukata suka yi imani. Amma fa alal-haqiqa su ne wawaye, sai dai ba su sani ba.**

**14 Idan suka haxu da muminai sai su ce,: Mun gasgata abin da kuka yi imani da shi. Suna faxin haka don tsoron muminai. Idan suka bar wurin muminai, suka koma wajen shugabanninsu, suka kaxaita da su, sai su ce - cikin tabbatar da biyayyarsu garesu -: Muna tare da ku akan tafarkinku, kawai muna nuna wa muminai a zahiri muna tare da su ne don izgili da reni gare su.**

**15 Allah yana mayar musu da izgilinsu da suke wa muminai, a matsayin sakamako gare su, na irin aikin da suke yi, don haka a nan duniya aka gudanar da hukunce-hukuncen musulmi a kansu, amma a lahira sai a saka musu da kafircinsu da munafincinsu. Haka Allah yake jinkirta wa kafirai don su zarce cikin vatansu da xagawarsu, su dauwama cikin ruxani da kai kawo.**

**16 Waxannan su ne wawaye, saboda sun canza imani da kafirci, don haka kasuwancinsu bai yi riba ba, saboda sun yi asarar imani da Allah, kuma ba sa kan shiriya.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Duk Wanxanda Allah ya rufe zuciyarsu saboda taurin kansu da qaryatawarsu, to komai girman ayoyi ba sa musu amfani. 2 - Jinkirtawar da Allah Maxaukaki Sarki yake wa azzalumai masu qaryatawa da ayoyinsa, ba wai don gafala ko gazawa ba ne, a'a yana jinkirta musu ne don su qara zunubi, kuma don azabarsu ta zama babba.**

مَثَلُهُمۡ كَمَثَلِ ٱلَّذِي ٱسۡتَوۡقَدَ نَارٗا فَلَمَّآ أَضَآءَتۡ مَا حَوۡلَهُۥ
ذَهَبَ ٱللَّهُ بِنُورِهِمۡ وَتَرَكَهُمۡ فِي ظُلُمَٰتٖ لَّا يُبۡصِرُونَ ١٧ صُمُّۢ
بُكۡمٌ عُمۡيٞ فَهُمۡ لَا يَرۡجِعُونَ ١٨ أَوۡ كَصَيِّبٖ مِّنَ ٱلسَّمَآءِ فِيهِ
ظُلُمَٰتٞ وَرَعۡدٞ وَبَرۡقٞ يَجۡعَلُونَ أَصَٰبِعَهُمۡ فِيٓ ءَاذَانِهِم مِّنَ
ٱلصَّوَٰعِقِ حَذَرَ ٱلۡمَوۡتِۚ وَٱللَّهُ مُحِيطُۢ بِٱلۡكَٰفِرِينَ ١٩ يَكَادُ ٱلۡبَرۡقُ
يَخۡطَفُ أَبۡصَٰرَهُمۡۖ كُلَّمَآ أَضَآءَ لَهُم مَّشَوۡاْ فِيهِ وَإِذَآ أَظۡلَمَ عَلَيۡهِمۡ
قَامُواْۚ وَلَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ لَذَهَبَ بِسَمۡعِهِمۡ وَأَبۡصَٰرِهِمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ
كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٢٠ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱعۡبُدُواْ رَبَّكُمُ ٱلَّذِي
خَلَقَكُمۡ وَٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَتَّقُونَ ٢١ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ
ٱلۡأَرۡضَ فِرَٰشٗا وَٱلسَّمَآءَ بِنَآءٗ وَأَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَأَخۡرَجَ
بِهِۦ مِنَ ٱلثَّمَرَٰتِ رِزۡقٗا لَّكُمۡۖ فَلَا تَجۡعَلُواْ لِلَّهِ أَندَادٗا وَأَنتُمۡ
تَعۡلَمُونَ ٢٢ وَإِن كُنتُمۡ فِي رَيۡبٖ مِّمَّا نَزَّلۡنَا عَلَىٰ عَبۡدِنَا فَأۡتُواْ
بِسُورَةٖ مِّن مِّثۡلِهِۦ وَٱدۡعُواْ شُهَدَآءَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ إِن
كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٢٣ فَإِن لَّمۡ تَفۡعَلُواْ وَلَن تَفۡعَلُواْ فَٱتَّقُواْ ٱلنَّارَ
ٱلَّتِي وَقُودُهَا ٱلنَّاسُ وَٱلۡحِجَارَةُۖ أُعِدَّتۡ لِلۡكَٰفِرِينَ ٢٤



**(17) Allah ya buga wa waxannan munafukai misalai guda biyu: misali na wuta, da misali na ruwa. Misali na wuta shi ne, su waxannan munafukai kamar wanda ya kunna wuta ne don ya ga haske da ita, da ta haska, ya yi zaton zai amfana da hasken, sai wutar da mutu, haskenta ya tafi, amma zafinta yana nan, ga kuma duhu ba sa ganin komai, ba sa gane hanya. (18) Sun zama bebaye kurame, ba sa jin gaskiya, ji na karva, kuma ba sa iya faxin gaskiya, sannan sun makance ba sa gani, ba sa barin vatan da suke kai.**

**(19) Amma misalinsu na ruwa: kamar ruwa ne mai yawa, tare da hadari mai xauke da duhu da tsawa da walkiya, ya sauka a kan wasu mutane, tsoro mai tsanani ya kama su, suka riqa rufe kunnuwansu da hannayensu, saboda tsananin qarar walkiya da tsoron mutuwa. Allah yana kewaye da kafirai, (ya san duk abin da suke aikatawa) ba za su gagare shi ba.**

**(20) Saboda tsananin hasken walqiyar, saura kaxan ta tafi da ganinsu, duk lokacin da ta haska sai su ci gaba da tafiya, idan ta xauke sai su tsaya, ba sa iya motsawa. Da Allah ya ga dama da ya tafiyar da jin su, da ganinsu, saboda cikakken ikon da yake da shi akan komai, ba za su qara gani ba, don bijirewar da suke yi wa gaskiya.**

**Ruwan saman shi ne kamar Alqur'ani. Qarar walqiya kuma shi ne misalin abin da yake cikin Alqur'ani na tsawatarwa. Hasken kuma da suke gani wani lokacin, shi ne misalin gaskiyar da take bayyana gare su wani lokaci. Toshe kunnuwansu kuwa da suke yi, shi ne misalin yadda suke bijirewa gaskiya da qin karvarta. Sannan inda munafukai suka yi kama da waxannan da Allah ya buga misali da su shi ne, wajen rashin amfanuwa. A misalin wuta, waxanda suka kunna wannan wuta ba su amfanu da komai ba, sai duhu da quna. A misalin ruwa kuwa, su ma ba su amfanu da komai ba, sai da abin da zai tsoratar da su na tsawa da walqiya. To haka ma Munafukai ba sa ganin komai dangane da addini sai tsanani da wahala.**

**Bayan Allah ya faxi kala-kalan mutane, muminai, kafirai, munafukai, sai kuma ya kira su gabaxaya zuwa ga kaxaita shi da bauta, Ya ce,: (21) Ya ku mutane ku bauta wa Ubangijinku shi kaxai, saboda shi ya halicce ku, ya halicci al'ummun da suke gabaninku, saboda ku sanya kariya tsakaninku da azabarsa, ta hanyar yin abubuwan da ya umarta, da barin abubuwan da ya hana.**

**(22) Shi ne wanda ya sanya muku qasa da zama shimfixa gare ku. Ya sanya sama mai kyan gini a saman qasar da kuke, shi ne wanda ya yi muku ni'imar saukar da ruwan sama, ya fitar da tsirrai kala-kala da wannan ruwan, don ya zama arziki gareku, don haka kada ku sanya wa Allah kishiyoyi, alhali kun san ba wanda ya yi halitta sai shi Allah Mai girma da buwaya.**

**(23) Ya ku mutane in kuna shakkar Alqur'anin da muka saukar wa da bawanmu Annabi Muhammad (S.A.W), to muna qalubalantarku, ku zo da sura guda xaya irinsa, wadda ta yi daidai da shi, ko da kuwa 'yar gajera ce. Ku kira duk wanda za ku iya kira cikin mataimakanku, in kuna da gaskiya cikin abin da kuke faxa.**

**(24) In ba ku yi haka ba – ba ma zaku iya ba – to ku ji tsoron wata wuta, da ake rurata da mutanen da suka cancanta a yi musu azaba, da duwatsu kala-kala, irin duwatsun suke bautawa da waninsu. Wannan wutar an tanade ta ne saboda Kafirai.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Allah yana tavar da munafukai a lokacin da suke cikin tsananin buqatar taimako, sakamakon munafuncinsu da bijirewarsu ga shiriya. 2 - Daga cikin manya-manyan dalilan da suke nuna wajabcin bautawa Allah shi kaxai, shi ne, kasancewarsa Shi ya halitta mana duk abin da yake duniya, ya kuma hore shi garemu. 3 - Gazawar halitta gabaxaya wajen iya zuwa da irin sura xaya ta Alqur'ani, yana nuna cewa wannan Alqur'ani Allah mai ilimi da hikima ne ya saukar da shi.**

وَبَشِّرِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أَنَّ لَهُمۡ جَنَّٰتٖ
تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُۖ كُلَّمَا رُزِقُواْ مِنۡهَا مِن ثَمَرَةٖ
رِّزۡقٗا قَالُواْ هَٰذَا ٱلَّذِي رُزِقۡنَا مِن قَبۡلُۖ وَأُتُواْ بِهِۦ مُتَشَٰبِهٗاۖ
وَلَهُمۡ فِيهَآ أَزۡوَٰجٞ مُّطَهَّرَةٞۖ وَهُمۡ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٢٥ ۞إِنَّ الحزب ١
ٱللَّهَ لَا يَسۡتَحۡيِۦٓ أَن يَضۡرِبَ مَثَلٗا مَّا بَعُوضَةٗ فَمَا فَوۡقَهَاۚ فَأَمَّا
ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ فَيَعۡلَمُونَ أَنَّهُ ٱلۡحَقُّ مِن رَّبِّهِمۡۖ وَأَمَّا
ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فَيَقُولُونَ مَاذَآ أَرَادَ ٱللَّهُ بِهَٰذَا مَثَلٗاۘ
يُضِلُّ بِهِۦ كَثِيرٗا وَيَهۡدِي بِهِۦ كَثِيرٗاۚ وَمَا يُضِلُّ بِهِۦٓ
إِلَّا ٱلۡفَٰسِقِينَ ٢٦ ٱلَّذِينَ يَنقُضُونَ عَهۡدَ ٱللَّهِ مِنۢ بَعۡدِ
مِيثَٰقِهِۦ وَيَقۡطَعُونَ مَآ أَمَرَ ٱللَّهُ بِهِۦٓ أَن يُوصَلَ وَيُفۡسِدُونَ
فِي ٱلۡأَرۡضِۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ٢٧ كَيۡفَ
تَكۡفُرُونَ بِٱللَّهِ وَكُنتُمۡ أَمۡوَٰتٗا فَأَحۡيَٰكُمۡۖ ثُمَّ يُمِيتُكُمۡ
ثُمَّ يُحۡيِيكُمۡ ثُمَّ إِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ ٢٨ هُوَ ٱلَّذِي خَلَقَ
لَكُم مَّا فِي ٱلۡأَرۡضِ جَمِيعٗا ثُمَّ ٱسۡتَوَىٰٓ إِلَى ٱلسَّمَآءِ
فَسَوَّىٰهُنَّ سَبۡعَ سَمَٰوَٰتٖۚ وَهُوَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٞ ٢٩



**(25) Kasancewar wancan alqawarin azaba ne ga kafirai, don haka ya kai wannan Annabi ka yi wa waxanda suka yi imani da Allah, suka yi ayyuka nagari, ka yi musu bushara da abin da zai faranta musu rai na Aljanna, waxanda qoramu suke gudana a qarqashin gine-ginenta da bishiyoyinta. A duk lokacin da aka ciyar da su wani xan itace a cikinta, sai ka ji sun ce, Wannan ai irin wanda aka ba mu ne a baya, saboda tsananin kama da ya yi da na duniya. An basu yayan itatuwan da sun yi kama da na duniya, don su karva, saboda sun san su, amma fa sun sha bamban da su a xanxano da daxi. Suna da mata waxanda suka kuvuta daga dukkan abin da rai ba ta so, na qazanta irin na duniya. Suna cikin ni'ima dauwamammiya, wadda ba ta yankewa, savanin ni'imar duniya mai yankewa.**

**(26) Allah ba ya kunyar buga misalai da abin da ya ga dama, yana buga misali da sauro da abin da ya fi shi girma, ko wanda bai kai shi ba.**

**Mutane sun kasu gida biyu dangane da irin wannan misalai, muminai da kafirai. Su muminai sun ba da gaskiya, sun san cewa akwai hikima a cikin hakan. Amma kafirai sai su yi ta izgili suna tambaye-tambaye akan mene ne na buga misali da abu wulaqantacce kamar Sauro da quda da Gizo-gizo da sauransu.**

**A cikin irin waxannan misalai akwai faxakarwa da jarraba wa ga mutane, a cikinsu akwai waxanda Allah yake vatar da su da waxannan misalai, saboda bijirewarsu daga lura da su. Wasu mutanen masu yawa kuwa Allah yana shiryarsu da su, saboda suna wa'azantuwa da waxannan misalai. Ba waxanda suke vacewa sai waxanda suka cancanta su vace, su ne waxanda suka qi yi wa Allah xa'a, kamar Munafukai.**

**(27) Su ne waxanda suke warware alqawarin da suka xaukar wa Allah, na za su bauta masa shi kaxai, za su bi Manzonsa, wanda Manzanni suka bada labarin zai zo. Waxannan masu warware alqawarin suna yanke abin da Allah ya yi umarni a sadar da shi, kamar zumunci, suna yaxa varna da zunubi a bayan-qasa. Waxannan su ne waxanda rabonsu ya yi qaranci a duniya da lahira.**

**(28) Lamarin – waxannan kafirai – akwai abun mamaki! Ta yaya kuke kafirce wa Allah, alhali kuna ganin abubuwan da suke nuna ikonsa a jikinku, domin kuwa da, babu ku, Allah ya samar da ku, ya raya ku, sannan shi ne yake kashe ku, kashewa ta biyu, sannan ya raya ku, rayawa ta biyu, sannan ya mayar da ku, don ya yi muku hisabi a kan abin da kuka gabatar.**

**(29) Dukkan abin da yake bayan qasa na bishiyoyi da qoramu da sauran abubuwan da ba wanda ya san adadinsu, Allah ne kaxai ya halitta muku su, kuna amfani da su, kuna jin daxi da hore muku su da ya yi. Sannan ya xaga sama, ya yi ta, hawa bakwai daidaitacciya, kuma shi ne wanda iliminsa ya kewaye da dukkan komai.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Saboda cikar ni'imar Aljannah, babu abin da yake vata jin daxinta, kuma babu wata cuta a cikinta.**

**2 - Babu wanda yake amfanuwa da misalan da Allah yake bugawa sai muminai, saboda su ne waxanda suke son shiriya da gaskiya, kuma suke nemanta da gaske.**

**3 - Yana daga mafi bayyanar siffofin Munafukai warware alqawari tsakaninsu da Allah, da tsakaninsu da mutane, da yanke abin da Allah ya yi umarni a sada shi, da yin varna a bayan qasa.**

**4 - Asalin abubuwa masu tsarki ne, kuma halal ne a yi amfani da su, saboda Allah ya yi wa bayinsa kyauta ne, ta halitta musu dukkan abin da yake bayan qasa.**

وَإِذۡ قَالَ رَبُّكَ لِلۡمَلَٰٓئِكَةِ إِنِّي جَاعِلٞ فِي ٱلۡأَرۡضِ خَلِيفَةٗۖ قَالُوٓاْ
أَتَجۡعَلُ فِيهَا مَن يُفۡسِدُ فِيهَا وَيَسۡفِكُ ٱلدِّمَآءَ وَنَحۡنُ نُسَبِّحُ
بِحَمۡدِكَ وَنُقَدِّسُ لَكَۖ قَالَ إِنِّيٓ أَعۡلَمُ مَا لَا تَعۡلَمُونَ ٣٠ وَعَلَّمَ
ءَادَمَ ٱلۡأَسۡمَآءَ كُلَّهَا ثُمَّ عَرَضَهُمۡ عَلَى ٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ فَقَالَ
أَنۢبِـُٔونِي بِأَسۡمَآءِ هَٰٓؤُلَآءِ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٣١ قَالُواْ سُبۡحَٰنَكَ
لَا عِلۡمَ لَنَآ إِلَّا مَا عَلَّمۡتَنَآۖ إِنَّكَ أَنتَ ٱلۡعَلِيمُ ٱلۡحَكِيمُ ٣٢ قَالَ يَٰٓـَٔادَمُ
أَنۢبِئۡهُم بِأَسۡمَآئِهِمۡۖ فَلَمَّآ أَنۢبَأَهُم بِأَسۡمَآئِهِمۡ قَالَ أَلَمۡ أَقُل
لَّكُمۡ إِنِّيٓ أَعۡلَمُ غَيۡبَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَأَعۡلَمُ مَا تُبۡدُونَ
وَمَا كُنتُمۡ تَكۡتُمُونَ ٣٣ وَإِذۡ قُلۡنَا لِلۡمَلَٰٓئِكَةِ ٱسۡجُدُواْ لِأٓدَمَ
فَسَجَدُوٓاْ إِلَّآ إِبۡلِيسَ أَبَىٰ وَٱسۡتَكۡبَرَ وَكَانَ مِنَ ٱلۡكَٰفِرِينَ ٣٤ وَقُلۡنَا
يَٰٓـَٔادَمُ ٱسۡكُنۡ أَنتَ وَزَوۡجُكَ ٱلۡجَنَّةَ وَكُلَا مِنۡهَا رَغَدًا حَيۡثُ
شِئۡتُمَا وَلَا تَقۡرَبَا هَٰذِهِ ٱلشَّجَرَةَ فَتَكُونَا مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ٣٥ فَأَزَلَّهُمَا
ٱلشَّيۡطَٰنُ عَنۡهَا فَأَخۡرَجَهُمَا مِمَّا كَانَا فِيهِۖ وَقُلۡنَا ٱهۡبِطُواْ بَعۡضُكُمۡ
لِبَعۡضٍ عَدُوّٞۖ وَلَكُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ مُسۡتَقَرّٞ وَمَتَٰعٌ إِلَىٰ حِينٖ ٣٦ فَتَلَقَّىٰٓ
ءَادَمُ مِن رَّبِّهِۦ كَلِمَٰتٖ فَتَابَ عَلَيۡهِۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ٣٧

**(30) Allah yana ba da labarin ya cewa Mala'iku: "Zan sanya mutane a bayan qasa, waxanda sashensu zai riqa maye gurbin sashe, saboda su raya bayan qasa da biyayya ga Allah". Sai Mala'iku suka tambayi Ubangijinsu, "me ye hikimar sanya 'ya'yan adam a bayan qasa, alhali za su yi varna, su zubar da jini a cikinta". Suka ci gaba da cewa, " Sannan mu muna maka xa'a, muna tsarkake ka, muna gode maka, muna girmama ka, ba ma gajiya". Sai Allah ya ba su amsa, ya ce, "Na san abin da baku sani ba, na hikima da manufofi masu girma wajen sanya su mamaya a bayan qasa".**

**(31) Saboda Allah ya nuna matsayin Annabi Adamu (A.S) sai ya sanar da shi sunayen dukkan abubuwa, dabbobi da sauran abubuwa, ya sanar da shi lafazansu da ma'anoninsu. Sannan ya bijirar da waxannan abubuwa ga Mala'iku, ya ce musu, "In da gaske ne abin da kuke faxa, cewa kun fi waxannan halitta falala, to ku bani labarin sunayen waxannan abubuwa".**

**(32) Sai suka ce – suna masu mayar da falala zuwa ga Allah da tabbatar da gazawarsu – "Tsarki ya tabbata gare ka, muna girmamaka ya Ubangijinmu, ba ma jayayya akan abin da ka hukunta ka kuma shar'anta, ba mu san komai ba, sai abin da ka azurta mu da saninsa. Kai ne masani, wanda babu wani abin da yake voyuwa a gare shi. Mai hikima, wanda kake sa al'amura a wurin da suka dace, da ikonka da shar'antawarka".**

**(33) Daga nan sai Allah ya ce wa Adam: Faxa musu sunayen waxannan abubuwa. Da ya faxa musu sunayen, kamar yadda Ubangijinsa ya sanar da shi. Sai Allah ya ce wa Mala'iku, Da ma ban faxa muku cewa na san duk abin da ya voyu a samai da qassai ba. Na san abin da kuka bayyana na halayenku da abin da yake cikin ranku. (34) Allah ya bayyana cewa ya umarci Mala'iku su yi wa Adam sujjada, ta girmamawa da ban-girma. Sai suka yi gaggawa wajen bin Allah, suka yi sujjadar. Sai Iblisu wanda Aljani ne, ya qi yin sujjadar, ya ja da umarnin Allah, na cewa ya yi wa Annabi Adam sujjada, saboda girman kai, don haka sai ya zama cikin waxanda suka kafirce wa Allah Maxaukakin Sarki.**

**(35) Mu ka ce, Ya Adamu, ku zauna a cikin Aljannah kai da matarka, ku ci daga abin da yake cikinta a ko'ina, hankalinku a kwance, cikin jin daxi, amma kada ku kusanci wannan bishiyar, wadda na hana ku cin ta, idan kuwa kuka kusanceta, to zaku zama cikin azzalumai, ta hanyar savawa abin da na umarce ku da shi.**

**(36) Shaixan bai gushe ba yana sanya musu kokwanto, yana qawata musu aikata abin da aka hana su, har sai da ya jefa su cikin laifi da zunubi, da hanyar cin wannan bishiyar da Allah ya hana su, don haka sai sakamakonsu ya kasance Allah ya fitar da su daga cikin Aljannar da suke ciki. Sannan Allah ya ce musu, su da Shaixan xin, Ku sauka zuwa bayan qasa, sashenku yana abokin gaba da sashe, kuna da wurin zama a bayan qasa, da jin daxi da abin da yake cikinta na alheri, har ajalinku ya zo, alqiyama ta tashi.**

**(37) Sai Annabi Adam ya faxi abin da Allah ya jefa masa na Kalmomi, waxanda ya kimsa masa addu'a da su, su ne kalmomin da Allah ya faxa, inda yake cewa: ((Suka ce, RABBANA ZALAMNA AMFUSANA, WA ILLAM TAGFIR LANA WA TARHAMNA LANA KUU NANNA MINAL KHAASIRIIN)). Sai Allah ya karvi tubansa, ya gafarta masa. Domin Shi Allah mai yawan karvar tuban bayi ne, mai jinqan su ne.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Abin da yake wajibi akan mumini idan bai gane hikimar Allah a cikin wasu halittunsa da lamarinsa ba, to ya sallama wa Allah cikin wannan halittar da lamarin. 2 - Alqur'ani ya xaga matsayin ilimi, ya sanya shi dalilin fifiko tsakanin halitta.**

**3 - Girman kai, shi ne shugaban zunubai, kuma tushen duk wani bala'i da yake sauka ga mutane, kuma shi ne farkon savon da aka savawa Allah da shi.**

قُلْنَا اهْبِطُوا مِنْهَا جَمِيعًا فَإِمَّا يَأْتِيَنَّكُم مِّنِّي هُدًى فَمَن تَبِعَ
هُدَايَ فَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ٣٨ وَالَّذِينَ كَفَرُوا
وَكَذَّبُوا بِآيَاتِنَا أُولَٰئِكَ أَصْحَابُ النَّارِ ۖ هُمْ فِيهَا خَالِدُونَ ٣٩
يَا بَنِي إِسْرَائِيلَ اذْكُرُوا نِعْمَتِيَ الَّتِي أَنْعَمْتُ عَلَيْكُمْ وَأَوْفُوا بِعَهْدِي
أُوفِ بِعَهْدِكُمْ وَإِيَّايَ فَارْهَبُونِ ٤٠ وَآمِنُوا بِمَا أَنزَلْتُ مُصَدِّقًا
لِّمَا مَعَكُمْ وَلَا تَكُونُوا أَوَّلَ كَافِرٍ بِهِ ۖ وَلَا تَشْتَرُوا بِآيَاتِي
ثَمَنًا قَلِيلًا وَإِيَّايَ فَاتَّقُونِ ٤١ وَلَا تَلْبِسُوا الْحَقَّ بِالْبَاطِلِ وَتَكْتُمُوا
الْحَقَّ وَأَنتُمْ تَعْلَمُونَ ٤٢ وَأَقِيمُوا الصَّلَاةَ وَآتُوا الزَّكَاةَ
نصف الحزب ١ وَارْكَعُوا مَعَ الرَّاكِعِينَ ٤٣ ۞ أَتَأْمُرُونَ النَّاسَ بِالْبِرِّ
وَتَنسَوْنَ أَنفُسَكُمْ وَأَنتُمْ تَتْلُونَ الْكِتَابَ ۚ أَفَلَا تَعْقِلُونَ ٤٤
وَاسْتَعِينُوا بِالصَّبْرِ وَالصَّلَاةِ ۚ وَإِنَّهَا لَكَبِيرَةٌ إِلَّا عَلَى الْخَاشِعِينَ
٤٥ الَّذِينَ يَظُنُّونَ أَنَّهُم مُّلَاقُو رَبِّهِمْ وَأَنَّهُمْ إِلَيْهِ رَاجِعُونَ ٤٦
يَا بَنِي إِسْرَائِيلَ اذْكُرُوا نِعْمَتِيَ الَّتِي أَنْعَمْتُ عَلَيْكُمْ وَأَنِّي فَضَّلْتُكُمْ
عَلَى الْعَالَمِينَ ٤٧ وَاتَّقُوا يَوْمًا لَّا تَجْزِي نَفْسٌ عَن نَّفْسٍ شَيْئًا
وَلَا يُقْبَلُ مِنْهَا شَفَاعَةٌ وَلَا يُؤْخَذُ مِنْهَا عَدْلٌ وَلَا هُمْ يُنصَرُونَ ٤٨



**(38) Muka ce da su, ku sauka gaba xayanku daga Aljannah zuwa qasa. Idan shiriya ta zo muku daga Manzannina, wanda ya bi, ya yi imani da Manzannina, to babu tsoro a kansu a lahira, kuma ba za su yi baqin ciki ba a kan abin da ya wuce su a duniya.**

**(39) Amma waxanda suka kafirta, suka qaryata da ayoyinmu, waxannan su ne 'yan wuta, waxanda za su zauna a cikinta.**

**(40) Ya ku 'ya 'yan Annabin Allah Yaqub, ku tuna ni'imar Allah mai yawa a kanku, ku gode mata, ku cika alqawarin da kuka yi min, na yin imani da ni, da Manzannina, da aiki da shari'o'ina. Idan kuka cika wannan alqawari Ni ma zan cika muku abin da na yi muku alqawari da shi, na rayuwa mai daxi a duniya, da sakamako mai kyau a ranar Alqiyama. Kuma ku ji tsorona ni kaxai, ka da ku warware alqawarina.**

**(41) Ku yi imani da Alqur'anin da na saukar ga Annabi Muhammad (S.A.W), wanda ya dace da abin da ya zo a cikin Attaura na kaxaita Allah da Annabcin Annabi Muhammad (S.A.W) kafin a canzata. Ku kiyaye, kada ku zama farkon jama'ar da za su kafirce. Kada ku canza ayoyina waxanda na saukar da 'yan kuxi kaxan, ko mulki ko matsayi. Ku kiyayi fushina da azabata.**

**(42) Kada ku cakuxa gaskiyar da na saukar wa Manzannina da abin da kuka qirqiro na qarya. Kada ku voye gaskiyar da ta zo a littafanku na siffar Annabi Muhammad (S.A.W), bayan ku san shi, kun tabbatar da shi.**

**(43) Ku cika sallah, da rukunanta da wajibanta, da sunnoninta. Ku bada zakkar dukiyoyinku, wadda Allah ya sa ta a hannunku. Ku qasqantar da kai ga Allah tare da masu qasqantar wa daga al'ummar Annabi Muhammad (S.A.W).**

**(44) Ba abin da ya fi muni irin ku umarci waninku da imani da aikata alheri, sannan ku, ku bijire, ku qi yi, ku manta da kawunanku, alhali kuna karanta Attaura, kuna sane da abin da yake cikinta na umarni da bin addinin Allah, da gasgata Manzanninsa. Yanzu ba za ku yi amfani da hankulanku ba?!.**

**(45) Ku nemi taimako akan al'amuranku na addini da na duniya ta hanyar haquri da sallah, wadda zata kusantar daku ga Allah, ta sada ku da shi, sai ya taimake ku, ya kiyaye ku, ya tafiyar muku da abin da yake tare da ku na cuta. Sallah tana da wuya da girma, sai dai ga waxanda suke qasqantar da kansu ga Ubangijinsu.**

**(46) Saboda su ne suka yi yaqinin zasu koma zuwa ga Ubangijinsu, za su haxu da shi ranar Alqiyama, su koma zuwa gare shi, don ya saka musu a kan ayyukansu.**

**(47) Ya ku 'ya 'yan Yaqub, ku tuna ni'imar addini da ta duniya da na yi muku. Ku tuna na fifita ku da annabci da mulkia kan mutanen zamaninku.**

**(48) Ku sanya kariya tsakaninku da azabar ranar alqiyama, ta hanyar aikata umarni da barin abubuwan da aka hana. A wannan ranar da wata rai bata wadata wa wata rai da komai, kuma ba za a karvi ceton wani a kan wani ba, wajen kawo masa amfani ko kawar masa da cuta, sai dai da izinin Allah. Kuma ba za a karvi fansa ba, koda kuwa zinare ne cikin bayan qasa. Basu da mataimaki a wannan rana. To idan mai ceto bai yi amfani ba, fansa da maitamaki ba su yi amfani ba, to ina mafita?!.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Tavewa ce mafi girma mutum ya umarci waninsa da aikin kirki, shi kuma ya manta da kansa. 2 - Haquri da Sallah suna cikin manya-manyan abubuwan da suke taimakon bawa a cikin dukkan sha'aninsa. 3 - A ranar alqiyama masu ceto ko fansa, ba sa kawar wa da mutum azaba, babu abin da zai amfane shi, sai aiki nagari.**

وَإِذۡ نَجَّيۡنَٰكُم مِّنۡ ءَالِ فِرۡعَوۡنَ يَسُومُونَكُمۡ سُوٓءَ ٱلۡعَذَابِ
يُذَبِّحُونَ أَبۡنَآءَكُمۡ وَيَسۡتَحۡيُونَ نِسَآءَكُمۡۚ وَفِي ذَٰلِكُم بَلَآءٞ
مِّن رَّبِّكُمۡ عَظِيمٞ ٤٩ وَإِذۡ فَرَقۡنَا بِكُمُ ٱلۡبَحۡرَ فَأَنجَيۡنَٰكُمۡ
وَأَغۡرَقۡنَآ ءَالَ فِرۡعَوۡنَ وَأَنتُمۡ تَنظُرُونَ ٥٠ وَإِذۡ وَٰعَدۡنَا مُوسَىٰٓ
أَرۡبَعِينَ لَيۡلَةٗ ثُمَّ ٱتَّخَذۡتُمُ ٱلۡعِجۡلَ مِنۢ بَعۡدِهِۦ وَأَنتُمۡ ظَٰلِمُونَ
٥١ ثُمَّ عَفَوۡنَا عَنكُم مِّنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ لَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ٥٢
وَإِذۡ ءَاتَيۡنَا مُوسَى ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡفُرۡقَانَ لَعَلَّكُمۡ تَهۡتَدُونَ ٥٣
وَإِذۡ قَالَ مُوسَىٰ لِقَوۡمِهِۦ يَٰقَوۡمِ إِنَّكُمۡ ظَلَمۡتُمۡ أَنفُسَكُم بِٱتِّخَاذِكُمُ
ٱلۡعِجۡلَ فَتُوبُوٓاْ إِلَىٰ بَارِئِكُمۡ فَٱقۡتُلُوٓاْ أَنفُسَكُمۡ ذَٰلِكُمۡ
خَيۡرٞ لَّكُمۡ عِندَ بَارِئِكُمۡ فَتَابَ عَلَيۡكُمۡۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلتَّوَّابُ
ٱلرَّحِيمُ ٥٤ وَإِذۡ قُلۡتُمۡ يَٰمُوسَىٰ لَن نُّؤۡمِنَ لَكَ حَتَّىٰ نَرَى ٱللَّهَ
جَهۡرَةٗ فَأَخَذَتۡكُمُ ٱلصَّٰعِقَةُ وَأَنتُمۡ تَنظُرُونَ ٥٥ ثُمَّ بَعَثۡنَٰكُم
مِّنۢ بَعۡدِ مَوۡتِكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ٥٦ وَظَلَّلۡنَا عَلَيۡكُمُ
ٱلۡغَمَامَ وَأَنزَلۡنَا عَلَيۡكُمُ ٱلۡمَنَّ وَٱلسَّلۡوَىٰۖ كُلُواْ مِن طَيِّبَٰتِ
مَا رَزَقۡنَٰكُمۡۚ وَمَا ظَلَمُونَا وَلَٰكِن كَانُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ٥٧



**(49) Ku tuna – Ya ku bani Isra'il – lokacin da muka tseratar da ku daga Fir'auna da mabiyansa, waxanda suke xanxana muku azaba kala-kala, suna yanka 'ya'yanku maza, don kada su rayu, suna barin 'ya'yanku mata don su yi musu hidima da bauta, kuma don su wulaqanta ku, su qasqanta ku. A cikin wannan tseratarwar da aka yi muku daga Fir'auna da mabiyansa akwai jarrabawa mai girma daga Ubangijinku, kuma an yi muku haka ne ko kwa godewa Allah Maxaukakarin Sarki.**

**(50) Ku tuna daga cikin ni'imomin da muka yi muku, mun raba muku kogi biyu, muka mayar shi hanya busasshiya, kuna tafiya a cikinta. Muka tseratar daku, muka halakar da maqiyinku Fir'auna da mabiyansa a gaban idonku, kuna kallonsu.**

**(51) Daga cikin irin waxannan ni'imomi ku tuna alqawarin da muka yi wa Annabi Musa na tsawon dare arba'in, saboda a qarasa saukar masa da Attaura a cikinsu, wadda take haske ce da shiriya. Amma sai kuka bautawa xan maraqi a wannan lokaci, kuna masu zalunci kanku da wannan aiki.**

**(52) Sai muka yafe muku bayan kun tuba, bamu kama ku ba, don ku godewa Allah ta hanyar kyautata xa'a da bauta gare shi.**

**(53) Ku tuna daga cikin irin waxannan ni'imomi mun baiwa Annabi Musa (A.S) Attaura, wadda take rarrabewa tsakanin gaskiya da varna, da bambance wa tsakanin shiriya da vata, ko kwa gane gaskiya da ita.**

**(54) Ku tuna, daga cikin irin waxannan ni'imomi ne, Allah ya datar da ku, kuka tuba daga bautar xan maraqi, yayin da Annabi Musa (A.S) ya ce da ku, "Kun zalunci kawunanku da kuka xauki xan Maraqi abin bautawa, don haka ku tuba zuwa ga Mahaliccinku, wanda ya samar da ku, sashenku ya kashe sashe. Irin wannan tuba ta fi alheri a kan ku zarce a kan kafirci, wanda zai kaiku dauwama a wuta". Sai kuka yi hakan, da taimakon Allah da datarwarsa, kuma Allah ya karvi tubanku, saboda shi mai yawan karvar tuba ne, kuma mai tausayin bayinsa ne.**

**(55) Ku tuna lokacin da iyayenku suka ce wa Annabi Musa (A.S) cikin qarfin hali, "Ba zamu yi imani da kai ba, har sai mun ga Allah a fili, ido-da-ido, babu wani shamaki!. Sai wuta mai zafi ta kama ku, ta kashe ku, sashenku yana kallon sashe.**

**(56) Sannan muka raya ku bayan mutuwarku, ko kwa godewa Allah akan wannan ni'ima da ya yi muku.**

**(57) Daga cikin ni'imomin da muka yi muku, mun aiko muku da girgije yana muku inuwa daga zafin rana, a lokacin da kuka vace a bayan qasa. Muka saukar muku da abin sha mai daxi kamar zuma, da tsuntsu mai daxin nama kamar Fakara. Muka ce da ku,: "Ku ci daga daxaxan abin da muka azurta ku da shi". Ba su tauye mu da komai ba yayin da suka yi musun waxannan ni'imomi, suka yi butulci, sai dai sun zalunci kansu, da hanyar rage wa kansu lada, da kuma bijirar da kansu ga azaba.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Girma da yawan ni'imomin da Allah ya yi wa bani Isra'ila, amma duk da haka ba su qara musu komai ba sai taurin kai da jayayya.**

**2 - Yalwar haqurin Allah da rahamarsa ga bayi, kome kuwa girman zunubansu.**

**3 - Wahayi shi ne yake rabe tsakanin gaskiya da qarya.**

وَإِذۡ قُلۡنَا ٱدۡخُلُواْ هَٰذِهِ ٱلۡقَرۡيَةَ فَكُلُواْ مِنۡهَا حَيۡثُ شِئۡتُمۡ
رَغَدٗا وَٱدۡخُلُواْ ٱلۡبَابَ سُجَّدٗا وَقُولُواْ حِطَّةٞ نَّغۡفِرۡ لَكُمۡ
خَطَٰيَٰكُمۡۚ وَسَنَزِيدُ ٱلۡمُحۡسِنِينَ ٥٨ فَبَدَّلَ ٱلَّذِينَ
ظَلَمُواْ قَوۡلًا غَيۡرَ ٱلَّذِي قِيلَ لَهُمۡ فَأَنزَلۡنَا عَلَى ٱلَّذِينَ ظَلَمُواْ
الحزب ١ رِجۡزٗا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ بِمَا كَانُواْ يَفۡسُقُونَ ٥٩ ۞ وَإِذِ ٱسۡتَسۡقَىٰ
مُوسَىٰ لِقَوۡمِهِۦ فَقُلۡنَا ٱضۡرِب بِّعَصَاكَ ٱلۡحَجَرَۖ فَٱنفَجَرَتۡ
مِنۡهُ ٱثۡنَتَا عَشۡرَةَ عَيۡنٗاۖ قَدۡ عَلِمَ كُلُّ أُنَاسٖ مَّشۡرَبَهُمۡۖ كُلُواْ
وَٱشۡرَبُواْ مِن رِّزۡقِ ٱللَّهِ وَلَا تَعۡثَوۡاْ فِي ٱلۡأَرۡضِ مُفۡسِدِينَ ٦٠
وَإِذۡ قُلۡتُمۡ يَٰمُوسَىٰ لَن نَّصۡبِرَ عَلَىٰ طَعَامٖ وَٰحِدٖ فَٱدۡعُ لَنَا
رَبَّكَ يُخۡرِجۡ لَنَا مِمَّا تُنۢبِتُ ٱلۡأَرۡضُ مِنۢ بَقۡلِهَا وَقِثَّآئِهَا
وَفُومِهَا وَعَدَسِهَا وَبَصَلِهَاۖ قَالَ أَتَسۡتَبۡدِلُونَ ٱلَّذِي هُوَ
أَدۡنَىٰ بِٱلَّذِي هُوَ خَيۡرٌۚ ٱهۡبِطُواْ مِصۡرٗا فَإِنَّ لَكُم مَّا سَأَلۡتُمۡۗ
وَضُرِبَتۡ عَلَيۡهِمُ ٱلذِّلَّةُ وَٱلۡمَسۡكَنَةُ وَبَآءُو بِغَضَبٖ مِّنَ
ٱللَّهِۗ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ كَانُواْ يَكۡفُرُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَيَقۡتُلُونَ
ٱلنَّبِيِّـۧنَ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّۗ ذَٰلِكَ بِمَا عَصَواْ وَّكَانُواْ يَعۡتَدُونَ ٦١



**(58) Ku tuna, daga cikin ni'imomin Allah a gare ku, mun ce da ku, "Ku shiga Baitil Muqaddas, ku ci abin da yake cikinsa na daxaxan abubuwa, cikin kwanciyar hankali da yalwa, a duk inda kuka so, amma yayin da za ku shiga ku shiga kuna masu sunkuyawa, masu qanqan da kai ga Allah, ku roqi Allah, kuna masu cewa, "Ubangijinmu ka yafe mana zunubanmu" zamu amsa muku. Kuma mu qarawa waxanda suka kyautata ayyukansu daga cikinku ladan kyautatawa.**

**(59) Amma sai waxanda suka zalunci kansu a cikinsu, suka canza aiki, suka canza abin da aka ce su faxa, suka shiga suna jan mazaunansu, suna cewa,, "Qwaya a cikin gashi" suna izgili da umarnin Allah. Don haka sai sakamakonsu ya kasance Allah ya saukar wa waxanda suka yi wannan zalunci azaba daga sama, saboda sun bar shari'a, kuma sun sava umarni.**

**(60) Ku tuna, daga cikin ni'imomin Allah a kanku, lokacin da kuke cikin ximuwa, qishirwa mai tsanani ta kama ku, sai Annabi Musa ya qanqantar da kai ga Allah, ya roqi Ubangijinsa ya shayar da ku, sai muka umarce shi da ya doki dutse da sandarsa, sai idanun ruwa goma sha biyu suka vuvvugo, adadin qabilunsu, ruwa ya fito. Muka bayyana wa kowace qabila wurin shan ruwanta, ita kaxai, don kada a samu savani a tsakaninsu. Muka ce da su, "Ku ci, ku sha, daga arzikin da Allah ya baku, ba tare da wata wahala ko aiki ba, amma kada ku yi varna a bayan qasa.**

**(61) Ku tuna lokacin da kuka butulce wa ni'imar Ubangijinku, ku ka qosa da abin da Allah ya saukar muku na abin sha mai daxi (darva) da nama mai daxi, kuka ce, "Ba za mu iya haquri akan cin abinci kala xaya ba, babu canji" don haka kuka nemi Annabi Musa (A.S) ya roqa muku Allah ya fitar muku da tsirran da suke bayan qasa, na daga kayan ganyenta da gurji, da Adas, da Albasa, su zama su ne abincinku. Sai Annabi Musa (A.S) ya ce da su- yana mai musu inkari -, "Yanzu zaku nemi canji da abin da yake qasqantacce, daga abin da ya fi alheri da karamci, kuma kuna samunsa ba tare da wata wahala ko gajiya ba: "To ku fita daga wannan qasar, zuwa kowace Alqarya, za ku samu abin da kuka tambaya a gonakinta da kasuwanninta. Amma saboda son zuciyarsu da bijirewarsu daga abin da Allah ya zava musu, sai wulaqanci da talauci da wahala suka same su, suka koma da fushin Allah, saboda barin addininsa, da kafirce wa ayoyinsa, da kashe Annabawansa kan zalunci da qetare iyaka, duk wannan abun ya same su ne, saboda sun savawa Allah, kuma sun qetare iyakokinsa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Duk wanda yake wasa da nassosin shari'a yana canza su yadda ya ga dama, to ya yi kama da Yahudawa, kuma ya jira azabar Allah.**

**2 - Girman falalar Allah ga Bani-Isra'ila. A gefe xaya kuma tsananin jayayarsu da taurin kansu da bijirewarsu ga barin Allah da shari'arsa.**

**3 - Yana daga cikin haxarin da savo da qetare iyaka suke kawo wa, qasqanci da wulaqanci su samu mutum, kuma abokan gaba su samu nasara a kansa.**

إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَٱلَّذِينَ هَادُواْ وَٱلنَّصَٰرَىٰ وَٱلصَّٰبِـِٔينَ مَنْ
ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْءَاخِرِ وَعَمِلَ صَٰلِحًا فَلَهُمْ أَجْرُهُمْ عِندَ
رَبِّهِمْ وَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ٦٢ وَإِذْ أَخَذْنَا
مِيثَٰقَكُمْ وَرَفَعْنَا فَوْقَكُمُ ٱلطُّورَ خُذُواْ مَآ ءَاتَيْنَٰكُم
بِقُوَّةٍ وَٱذْكُرُواْ مَا فِيهِ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ ٦٣ ثُمَّ تَوَلَّيْتُم
مِّنۢ بَعْدِ ذَٰلِكَ فَلَوْلَا فَضْلُ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَتُهُۥ لَكُنتُم مِّنَ
ٱلْخَٰسِرِينَ ٦٤ وَلَقَدْ عَلِمْتُمُ ٱلَّذِينَ ٱعْتَدَوْاْ مِنكُمْ فِى ٱلسَّبْتِ
فَقُلْنَا لَهُمْ كُونُواْ قِرَدَةً خَٰسِـِٔينَ ٦٥ فَجَعَلْنَٰهَا نَكَٰلًا لِّمَا
بَيْنَ يَدَيْهَا وَمَا خَلْفَهَا وَمَوْعِظَةً لِّلْمُتَّقِينَ ٦٦ وَإِذْ قَالَ
مُوسَىٰ لِقَوْمِهِۦٓ إِنَّ ٱللَّهَ يَأْمُرُكُمْ أَن تَذْبَحُواْ بَقَرَةً قَالُوٓاْ
أَتَتَّخِذُنَا هُزُوًا قَالَ أَعُوذُ بِٱللَّهِ أَنْ أَكُونَ مِنَ ٱلْجَٰهِلِينَ
٦٧ قَالُواْ ٱدْعُ لَنَا رَبَّكَ يُبَيِّن لَّنَا مَا هِىَ قَالَ إِنَّهُۥ يَقُولُ إِنَّهَا
بَقَرَةٌ لَّا فَارِضٌ وَلَا بِكْرٌ عَوَانٌۢ بَيْنَ ذَٰلِكَ فَٱفْعَلُواْ مَا
تُؤْمَرُونَ ٦٨ قَالُواْ ٱدْعُ لَنَا رَبَّكَ يُبَيِّن لَّنَا مَا لَوْنُهَا قَالَ إِنَّهُۥ
يَقُولُ إِنَّهَا بَقَرَةٌ صَفْرَآءُ فَاقِعٌ لَّوْنُهَا تَسُرُّ ٱلنَّٰظِرِينَ ٦٩



**(62) Duk wanda ya yi imani daga cikin wannan al'umma, haka ma daga cikin al'ummun da suka wuce kafin aiko da Annabi Muhammad (S.A.W) daga cikin Yahudawa da Nasara, da Sabi'awa (wasu mutane ne daga cikin mabiya wasu Annabawa da suka yi imani da Allah da ranar qarshe) to duk waxannan suna da ladansu a wurin Ubangijinsu, ba su da tsoron abin da za su fuskanta a lahira, ba su da kuma baqin cikin abin da ya wuce su a duniya.**

**(63) Ku tuna abin da muka yi alqawari mai qarfi da ku a kansa, na yin imani da Alllah da Manzanninsa, da yadda muka xaga dutse a kanku don tsoratar da ku da jan kunnenku a kan aiki da wannan alqawari. Muka umarce ku da ku riqe abin da muka saukar muku na Attaura da kyau, ba tare da sakaci ko kasala ba, ku kiyaye abin da yake cikinta, ku yi masa kyakkyawar fahimta, saboda ko kwa tsira daga azabar Allah idan kun aikata haka.**

**(64) Bayan duk haka ta faru, sai kawai kuka bijire, kuka kawar da kanku, kuka bar alqawarin da kuka xauka. Ba don falalar Allah a kanku ba, da yafe muku da ya yi, da rahamarsa na karvar tubanku, da kun zama cikin hasararru, saboda bijirewa da savawa.**

**(65) Kun san labarin waxanda suka gabace ku, sanin da babu kokwanto a cikinsa. Lokacin da suka qetare iyaka, suka riqa kama kifi ranar Assabar, ranar da aka haramta musu kama kifi a cikinta, sai suka yi dabara, suka riqa kafa tarkon kamun kifin kafin ranar Assabar xin, suna fitar da shi ranar lahadi. Sai Allah ya mayar da waxannan masu dabarar suka zama birrai, ababen qi, an musu haka ne uquba akan dabarar da suka yi.**

**(66) Sai muka sanya wannan alqaryar da ta qetare iyaka ta zama izina ga alqaryun da suke kusa da ita, da waxanda za su zo bayanta, don kada su yi aiki irin na ta, su cancanci uquba irin tata. Sannan muka sanya ta tunatarwa ga masu tsoron Allah, waxanda suke tsoron azabar Allah da kamunsa ga duk wanda ya qetare iyakarsa.**

**(67) Ku tuna daga labaran waxanda suka gabace ku, abin da ya faru tsakaninsu da Annabi Musa (A.S). A lokacin da ya faxa musu umarnin Allah na su yanka saniya daga cikin shanun da suke da su, maimakon su yi sauri, sai kawai suka ce, suna masu izgili, "Yanzu mu zaka mayar abokan izgilinka!" sai Annabi Musa ya ce da su, "Ina neman tsarin Allah kada in zama daga cikin waxanda suke wa Allah qarya, suke wa Mutane izgili".**

**(68) Suka ce da Annabi Musa: "Ka roqa mana Ubangijinka ya bayyana mana siffar saniyar da aka umarce mu, mu yanka". Sai ya ce musu, "Allah ya ce: Ita saniya ce wadda ba mai shekaru ba, ba kuma qarama ba, tsaka-tsakiya ce, ku gaggauta bin umarnin Ubangijinku".**

**(69) Sai suka ci gaba da jayayya da taurin kai, suka ce wa Annabi Musa,: "Ka roqa mana Ubangijinka ya faxa mana launinta". Sai Annabi Musa ya ce da su, "Allah yana cewa, "Ita saniya ce, mai fatsi-fatsin launi, wanda ya ciza, tana burge duk wanda ya kalle ta".**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Hukuncin da aka ambata a ayar farko, kafin aiko Annabi Muhammad (S.A.W) ne. Amma bayan aiko shi, addinin da Allah ya yarda da shi, shi ne Musulunci, ba zai karvi wani addini ba, wanda ba shi ba, kamar yadda Allah ya faxa, a wata ayar ya ce, (Duk wanda ya nemi wani addini ba musulunci ba, to ba za a karva daga gare shi ba, kuma a ranar alqiyama yana cikin hasararru) (Ali-Imran:Aya ta 85). 2 - Allah yana iya gaggauta azabar wasu zunubai a duniya tun kafin a je lahira, don hakan ya zama gargaxi da tunatarwa ga mutane, kuma don su ji tsoron savawa umarnin Allah.**
**3 - Duk wanda ya takurawa kansa, ya matsantawa kansa, a kan abin da yake da yalwa a cikinsa a shari'a, to za a iya masa uquba ta hanyar tsananta masa a cikin wannan abun.**

قَالُواْ ٱدۡعُ لَنَا رَبَّكَ يُبَيِّن لَّنَا مَا هِيَ إِنَّ ٱلۡبَقَرَ تَشَٰبَهَ عَلَيۡنَا وَإِنَّآ
إِن شَآءَ ٱللَّهُ لَمُهۡتَدُونَ ٧٠ قَالَ إِنَّهُۥ يَقُولُ إِنَّهَا بَقَرَةٞ لَّا ذَلُولٞ
تُثِيرُ ٱلۡأَرۡضَ وَلَا تَسۡقِي ٱلۡحَرۡثَ مُسَلَّمَةٞ لَّا شِيَةَ فِيهَاۚ قَالُواْ
ٱلۡـَٰٔنَ جِئۡتَ بِٱلۡحَقِّۚ فَذَبَحُوهَا وَمَا كَادُواْ يَفۡعَلُونَ ٧١ وَإِذۡ
قَتَلۡتُمۡ نَفۡسٗا فَٱدَّٰرَٰٔتُمۡ فِيهَاۖ وَٱللَّهُ مُخۡرِجٞ مَّا كُنتُمۡ تَكۡتُمُونَ ٧٢
فَقُلۡنَا ٱضۡرِبُوهُ بِبَعۡضِهَاۚ كَذَٰلِكَ يُحۡيِ ٱللَّهُ ٱلۡمَوۡتَىٰ وَيُرِيكُمۡ
ءَايَٰتِهِۦ لَعَلَّكُمۡ تَعۡقِلُونَ ٧٣ ثُمَّ قَسَتۡ قُلُوبُكُم مِّنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ
فَهِيَ كَٱلۡحِجَارَةِ أَوۡ أَشَدُّ قَسۡوَةٗۚ وَإِنَّ مِنَ ٱلۡحِجَارَةِ لَمَا يَتَفَجَّرُ
مِنۡهُ ٱلۡأَنۡهَٰرُۚ وَإِنَّ مِنۡهَا لَمَا يَشَّقَّقُ فَيَخۡرُجُ مِنۡهُ ٱلۡمَآءُۚ وَإِنَّ
مِنۡهَا لَمَا يَهۡبِطُ مِنۡ خَشۡيَةِ ٱللَّهِۗ وَمَا ٱللَّهُ بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعۡمَلُونَ ٧٤
۞أَفَتَطۡمَعُونَ أَن يُؤۡمِنُواْ لَكُمۡ وَقَدۡ كَانَ فَرِيقٞ مِّنۡهُمۡ الحزب ٢
يَسۡمَعُونَ كَلَٰمَ ٱللَّهِ ثُمَّ يُحَرِّفُونَهُۥ مِنۢ بَعۡدِ مَا عَقَلُوهُ وَهُمۡ
يَعۡلَمُونَ ٧٥ وَإِذَا لَقُواْ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ قَالُوٓاْ ءَامَنَّا وَإِذَا
خَلَا بَعۡضُهُمۡ إِلَىٰ بَعۡضٖ قَالُوٓاْ أَتُحَدِّثُونَهُم بِمَا فَتَحَ ٱللَّهُ
عَلَيۡكُمۡ لِيُحَآجُّوكُم بِهِۦ عِندَ رَبِّكُمۡۚ أَفَلَا تَعۡقِلُونَ ٧٦



**(70) Sai suka ci gaba da taurin kansu, suka ce, "Ka roqa mana Ubangijinka ya qara bayyana mana siffofinta, saboda saniyar dake da waxannan siffofin da aka ambata tana da yawa, ba zamu iya gane ta ba daga cikin shanu". Suka qarfafa maganarsu da cewa Insha Allahu za su gane saniyar da ake so su yanka idan aka yi musu bayani.**

**(71) Sai Annabi Musa ya ce da su, "Allah ya ce, siffar wannan saniya ita ce, ba a horar da ita ba da aikin noma, ko shayar da shuka, qalau take, bata da wani aibu ko wani launi na daban in ba fatsi-fatsi ba. Daga nan sai suka ce, "Yanzu ka zo da siffofi na sosai, wadda zamu gane saniyar da su". Sannan sai suka yanka ta, bayan sun yi kamar ba za su yanka ba, saboda tsananin jayayya da taurin kai.**

**(72) Ku tuna lokacin da kuka kashe xaya daga cikinku, kuka yi turerreniyar laifi, kowa yana cewa ba shi ya kashe shi ba, yana tuhumar xan uwansa da kisan, kuka yi ta jayayya. Alhali Allah mai fitar da abin da kuke voyewa ne na kashe wanda ba ruwansa.**

**(73) Sai muka ce da su,: "ku doki wanda aka kashe da wani sashe na saniyar da aka umarce ku da yankawa, saboda Allah zai raya shi, ya faxa muku wanda ya yi kisan!". Sai suka aikata hakan, kuma ya basu labarin wanda ya yi kisan. To irin wannan raya mataccen, haka Allah yake raya waxanda suka mutu ranar alqiyama. Yana nuna muku dalilan da suke bayyana ikonsa, ko kwa hankalta ku yi imani na gaskiya da Allah Maxaukakin Sarki.**

**(74) Bayan duk waxannan wa'azozi da mu'ujizozi sai zukatanku suka qeqashe, har suka zama kamar duwatsu, kai! Suka fi duwatsu ma tsauri, domin ba sa canzawa a kowanne hali. Amma duwatsu suna canzawa, daga cikinsu, akwai waxanda qoramu suke vuvvugowa daga cikinsu, haka nan akwai waxanda suke tsagewa idanun ruwa su fitowa, suna gudana a bayan qasa, mutane da dabbobi suna amfani da shi, daga cikinsu akwai waxanda suke faxowa daga can saman duwatsu, don razana da tsoron Allah, amma zukatanku ba haka suke ba. Allah ba rafkananne ba ne akan abin da kuke aikatawa, yana sane, kuma zai saka muku da shi.**

**(75) Yanzu ku muminai bayan kun san halin Yahudu da taurin kansu, har kuna fatan za su yi imani, su amsa muku. Alhali wasu daga cikin malamansu suna jin zancen Allah, wanda ya saukar musu a cikin Attaura, amma sai su canza lafazinsa da ma'anoninsa, alhali sun fahimta, sun gane, kuma sun san girman laifin da suka aikata.**

**(76) Daga cikin tufka da warwarar Yahudawa shi ne, idan wasu daga cikinsu suka haxu da muminai, sai su tabbatar da gaskiyar Annabi Muhammad (S.A.W) da ingancin saqonsa, kuma shi ne abin da Attaura ta tabbatar. Amma idan sashensu ya kevanta da sashe, sai kuma su zargi juna akan abin da suka yi na tabbatar da Manzancin Annabi (S.A.W). saboda musulmai suna tsayar musu da hujja da abin da suka faxa na gaskiyar Annabta.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Zuciyar wasu bayin ta fi dutse qeqashewa, ba ta yin laushi saboda wa'azi, haka ma bata tausasa don tunatarwa.**

**2 - Dalilai da hujjoji, komai yawansu ba sa amfani, in zuciya ba ta miqa wuya ga Allah ba, bata qanqantar da kai gare shi ba.**

**3 - Ayoyin sun bayyana haqiqanin abin da Yahudawa suke voyewa a cikin zukatansu, ta yadda suka gaji yaudara da wasa da addini daga magabatansu.**

77 Waxannan Yahudawa suna yin waxannan munanan ayyukan ne, kamar sun gafala da cewa Allah yana sanin duk abin da suke voyewa na maganganunsu da ayyukansu, da abin da suka bayyana, kuma zai bayyana shi ga bayi, ya tozarta su.

78 Daga cikin Yahudawa, akwai wasu jama'a da basu san komai a Attaura ba, sai dai kawai su karanta ta, ba sa fahimtar abin da take koyarwa. Babu abin da yake tare da su, sai qarerayin da suka samo daga manyansu, suna xaukar cewa, su ne Attaurar da Allah ya saukar.

79 Azaba da halaka mai tsanani yake jiran waxannan, waxanda suke rubuta littafi da hannayensu, sannan su yi qarya su ce, wannan daga wurin Allah yake, don kawai su canza gaskiya da shiriya da xan kuxi kaxan a duniya, ko mulki. To azaba da halaka mai tsanani ta tabbata a kansu, saboda abin da hannayensu suka rubuta, da qaryar da suke wa Allah. Azaba da halaka mai tsanani sun tabbata a kansu, saboda abin da suke samu na dukiya da mulki da wannan aikin.

80 Suka faxa – suna masu qarya da ji-ji-da-kai -, "Wuta ba za ta shafe mu ba, ba zamu shige ta ba, sai yan kwanaki kaxan". Ya wannan Annabi ka ce da su, "Ko kun yi wani alqawari mai qarfi da Allah ne akan haka?" idan kuna da alqawari, to ku sani Allah baya sava alqawarinsa. Ko kuwa dai kuna faxawa Allah abin da baku sani ba ne, saboda qarya da shaidar zur.

81 To fa lamarin ba kamar yadda waxannan suke zato ba ne. lallai Allah yana azabtar da duk wanda ya aikata kafirci, zunubansa suka kewaye shi, yana saka musu, da shiga wuta, da dauwama a cikinta, har abada.

82 Waxanda suka yi imani da Allah da Manzonsa, suka aikata ayyuka nagartattu, to ladansu a wajen Allah shi ne ,shiga Aljannah da zama a cikinta har abada.

83 Ku tuna alqawarin nan mai qarfi da muka riqa a kanku, ya ku Bani Isra'ila, a kan zaku kaxaita Allah, ba za ku bautawa wani tare da shi ba, kuma zaku kyautatawa iyayenku da makusantanku, da marayu, da miskinai, da mabuqata, kuma zaku faxa wa mutane magana mai kyau, da umarni da kyakkyawan aiki, da hani da mummuna, ba tare da tsanantawa ko kausasawa ba, sannan zaku yi sallah cikakkiya, kamar yadda aka umarce ku, zaku ba da zakkah ga waxanda suka cancanceta, cikin jin daxi. Amma sai kuka warware wannan alqawari, kuka juya baya, kuka bijire daga alqawarin da aka riqa a kanku.



أَوَلَا يَعْلَمُونَ أَنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ مَا يُسِرُّونَ وَمَا يُعْلِنُونَ ٧٧
وَمِنْهُمْ أُمِّيُّونَ لَا يَعْلَمُونَ ٱلْكِتَٰبَ إِلَّآ أَمَانِيَّ وَإِنْ هُمْ
إِلَّا يَظُنُّونَ ٧٨ فَوَيْلٌ لِّلَّذِينَ يَكْتُبُونَ ٱلْكِتَٰبَ بِأَيْدِيهِمْ
ثُمَّ يَقُولُونَ هَٰذَا مِنْ عِندِ ٱللَّهِ لِيَشْتَرُوا۟ بِهِۦ ثَمَنًا قَلِيلًا ۖ
فَوَيْلٌ لَّهُم مِّمَّا كَتَبَتْ أَيْدِيهِمْ وَوَيْلٌ لَّهُم مِّمَّا يَكْسِبُونَ
٧٩ وَقَالُوا۟ لَن تَمَسَّنَا ٱلنَّارُ إِلَّآ أَيَّامًا مَّعْدُودَةً ۚ قُلْ
أَتَّخَذْتُمْ عِندَ ٱللَّهِ عَهْدًا فَلَن يُخْلِفَ ٱللَّهُ عَهْدَهُۥٓ ۖ أَمْ
تَقُولُونَ عَلَى ٱللَّهِ مَا لَا تَعْلَمُونَ ٨٠ بَلَىٰ مَن كَسَبَ سَيِّئَةً
وَأَحَٰطَتْ بِهِۦ خَطِيٓـَٔتُهُۥ فَأُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلنَّارِ ۖ هُمْ
فِيهَا خَٰلِدُونَ ٨١ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ
أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلْجَنَّةِ ۖ هُمْ فِيهَا خَٰلِدُونَ ٨٢ وَإِذْ أَخَذْنَا
مِيثَٰقَ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ لَا تَعْبُدُونَ إِلَّا ٱللَّهَ وَبِٱلْوَٰلِدَيْنِ
إِحْسَانًا وَذِى ٱلْقُرْبَىٰ وَٱلْيَتَٰمَىٰ وَٱلْمَسَٰكِينِ وَقُولُوا۟
لِلنَّاسِ حُسْنًا وَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُوا۟ ٱلزَّكَوٰةَ ثُمَّ
تَوَلَّيْتُمْ إِلَّا قَلِيلًا مِّنكُمْ وَأَنتُم مُّعْرِضُونَ ٨٣



## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

1 - Wasu daga cikin ma'abota littafi suna da'awar sanin abin da Allah ya saukar. Amma alal-haqiqa ba su da ilimin abin da Allah ya saukar, sai dai ruxu da jahilci.

2 - Daga cikin mutane, wanda ya fi kowa girman zunubi, shi ne wanda yake wa Allah da Manzanninsa qarya, ya danganta musu abin da ba daga gare su yake ba.

3 - Duk da girman alqawuran da Allah ya yi da Yahudu, da yadda aka qarfafa su, hakan bai qara musu komai ba sai bijirewa da qin cika waxannan alqawura.

وَإِذْ أَخَذْنَا مِيثَٰقَكُمْ لَا تَسْفِكُونَ دِمَآءَكُمْ وَلَا تُخْرِجُونَ
أَنفُسَكُم مِّن دِيَٰرِكُمْ ثُمَّ أَقْرَرْتُمْ وَأَنتُمْ تَشْهَدُونَ ٨٤
ثُمَّ أَنتُمْ هَٰٓؤُلَآءِ تَقْتُلُونَ أَنفُسَكُمْ وَتُخْرِجُونَ فَرِيقًا
مِّنكُم مِّن دِيَٰرِهِمْ تَظَٰهَرُونَ عَلَيْهِم بِٱلْإِثْمِ وَٱلْعُدْوَٰنِ
وَإِن يَأْتُوكُمْ أُسَٰرَىٰ تُفَٰدُوهُمْ وَهُوَ مُحَرَّمٌ عَلَيْكُمْ
إِخْرَاجُهُمْ ۚ أَفَتُؤْمِنُونَ بِبَعْضِ ٱلْكِتَٰبِ وَتَكْفُرُونَ بِبَعْضٍ ۚ
فَمَا جَزَآءُ مَن يَفْعَلُ ذَٰلِكَ مِنكُمْ إِلَّا خِزْىٌ فِى ٱلْحَيَوٰةِ
ٱلدُّنْيَا ۖ وَيَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ يُرَدُّونَ إِلَىٰٓ أَشَدِّ ٱلْعَذَابِ ۗ وَمَا ٱللَّهُ
بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعْمَلُونَ ٨٥ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ ٱشْتَرَوُا۟ ٱلْحَيَوٰةَ
ٱلدُّنْيَا بِٱلْءَاخِرَةِ ۖ فَلَا يُخَفَّفُ عَنْهُمُ ٱلْعَذَابُ وَلَا هُمْ يُنصَرُونَ
٨٦ وَلَقَدْ ءَاتَيْنَا مُوسَى ٱلْكِتَٰبَ وَقَفَّيْنَا مِنۢ بَعْدِهِۦ
بِٱلرُّسُلِ ۖ وَءَاتَيْنَا عِيسَى ٱبْنَ مَرْيَمَ ٱلْبَيِّنَٰتِ وَأَيَّدْنَٰهُ بِرُوحِ
ٱلْقُدُسِ ۗ أَفَكُلَّمَا جَآءَكُمْ رَسُولٌۢ بِمَا لَا تَهْوَىٰٓ أَنفُسُكُمُ
ٱسْتَكْبَرْتُمْ فَفَرِيقًا كَذَّبْتُمْ وَفَرِيقًا تَقْتُلُونَ ٨٧ وَقَالُوا۟ قُلُوبُنَا
غُلْفٌۢ ۚ بَلْ لَّعَنَهُمُ ٱللَّهُ بِكُفْرِهِمْ فَقَلِيلًا مَّا يُؤْمِنُونَ ٨٨



**(84) Ku tuna alqawarin nan mai qarfi da muka yi da ku a cikin Attaura na haramta wa sashe zubar da jinin sashe, da haramta wa sashenku fitar da sashe daga gidajensu, kuka tabbatar da wannan alqawarin da muka yi da ku, kuna masu shaida wa da ingancinsa.**

**(85) Sannan kuma sai kuka sava wannan alqawari, sashenku yana kashe sashe, kuma kuna fitar da wasu jama'a daga cikinku daga gidajensu, kuna taimaka wa maqiya a kansu, don zalunci da qetare iyaka. Sannan bayan sun zama ribatattun yaqi a wurin maqiya, sai kuma ku fanshe su, don ku kuvutar da su daga hannunsu, alhali an haramta muku fitar da su, to ta yaya kuke imani da wani sashe na Attaura, na fansar waxanda suke ribatattu, sannan kuma kuna kafirce wa da sashen da yake kare jini, ya hana sashenku fitar da sashe daga gidajensu, yaya haka?. Wanda duk yake aikata haka, ba shi da wani sakamako sai qasqanci da wulaqanci a rayuwar duniya. A lahira kuma za a mayar da shi zuwa ga mafi tsananin azaba. Allah bai gafala daga abin da kuke aikatawa ba, yana ganinku, kuma zai saka muku.**

**(86) Waxannan su ne waxanda suka canza rayuwar lahira da ta duniya, suka zavi mai qarewa akan mai dauwama, don haka ba za a sauqaqa musu azaba ba a Lahira, kuma ba su da wani mataimaki da zai taimake su a ranar.**

**(87) Haqiqa mun baiwa Annabi Musa Attaura, sannan muka biyo bayansa da Manzanni. Muka ba wa Annabi Isa xan Maryam ayoyi bayyanannu, waxanda suke tabbbatar da gaskiyarsa, kamar raya matattatu, da warkar da kutare, da masu kora. Muka qarfafa shi da Mala'ika Jibrilu. Amma duk lokacin da wani Annabi ya zo muku – Ya bani Isra'il –daga wajen Allah, da abin da bai dace da son zuciyarku ba, sai ku yi girman kai a kan gaskiya, da koyarwa Annabawan Allah gare ku. Ku qaryata wasu, wasu kuma ku kashe su?!.**

**(88) Hujjar Yahudawa ta qin bin Annabi Muhammad (S.A.W) ita ce, "Mu zukatanmu a rufe suke, babu abin da yake shigar su, daga abin da kake faxa, ba ma fahimta". Amma ba haka abin yake ba, kamar yadda suke rayawa, Allah ne dai ya kore su daga rahamarsa, saboda kafircinsu, don haka ba zasu yi imani ba sai da xan kaxan daga abin da Allah ya saukar.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yana daga mafi girman kafirci, imani da wani sashe na abin da Allah ya saukar, da kafircewa sashe, domin duk wanda ya yi haka, to ya mayar da son zuciyarsa Allansa.**

**2 - Tsananin taurin kan Yahudawa, da bin son zuciyarsu, da wasa da abin da Allah Maxaukakin Sarki ya saukar.**

**3 - Falalar Allah da rahamarsa ga halittarsa, ta yadda ya ci gaba da aiko da manzanni da saukar da littafai don shiryar da su**

**4 - Allah yana yin azaba ga waxanda suka bijirewa shiriya, suka yi taurin kai, ga barin umarninsa, ta hanyar rufe zukatansu, da korar su daga rahamarsa, don haka ba sa shiriya zuwa ga gaskiya, kuma ba sa aiki da ita.**

وَلَمَّا جَآءَهُمۡ كِتَٰبٞ مِّنۡ عِندِ ٱللَّهِ مُصَدِّقٞ لِّمَا مَعَهُمۡ
وَكَانُواْ مِن قَبۡلُ يَسۡتَفۡتِحُونَ عَلَى ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فَلَمَّا
جَآءَهُم مَّا عَرَفُواْ كَفَرُواْ بِهِۦۚ فَلَعۡنَةُ ٱللَّهِ عَلَى ٱلۡكَٰفِرِينَ
٨٩ بِئۡسَمَا ٱشۡتَرَوۡاْ بِهِۦٓ أَنفُسَهُمۡ أَن يَكۡفُرُواْ بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ
بَغۡيًا أَن يُنَزِّلَ ٱللَّهُ مِن فَضۡلِهِۦ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ مِنۡ عِبَادِهِۦۖ
فَبَآءُو بِغَضَبٍ عَلَىٰ غَضَبٖۚ وَلِلۡكَٰفِرِينَ عَذَابٞ مُّهِينٞ
٩٠ وَإِذَا قِيلَ لَهُمۡ ءَامِنُواْ بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ قَالُواْ نُؤۡمِنُ بِمَآ أُنزِلَ
عَلَيۡنَا وَيَكۡفُرُونَ بِمَا وَرَآءَهُۥ وَهُوَ ٱلۡحَقُّ مُصَدِّقٗا لِّمَا
مَعَهُمۡۗ قُلۡ فَلِمَ تَقۡتُلُونَ أَنۢبِيَآءَ ٱللَّهِ مِن قَبۡلُ إِن كُنتُم
مُّؤۡمِنِينَ ٩١ ۞ وَلَقَدۡ جَآءَكُم مُّوسَىٰ بِٱلۡبَيِّنَٰتِ ثُمَّ ربع الحزب
ٱتَّخَذۡتُمُ ٱلۡعِجۡلَ مِنۢ بَعۡدِهِۦ وَأَنتُمۡ ظَٰلِمُونَ ٩٢ وَإِذۡ
أَخَذۡنَا مِيثَٰقَكُمۡ وَرَفَعۡنَا فَوۡقَكُمُ ٱلطُّورَ خُذُواْ
مَآ ءَاتَيۡنَٰكُم بِقُوَّةٖ وَٱسۡمَعُواْۖ قَالُواْ سَمِعۡنَا وَعَصَيۡنَا
وَأُشۡرِبُواْ فِي قُلُوبِهِمُ ٱلۡعِجۡلَ بِكُفۡرِهِمۡۚ قُلۡ بِئۡسَمَا
يَأۡمُرُكُم بِهِۦٓ إِيمَٰنُكُمۡ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ٩٣



**89** **Yayin da Alqur'ani mai girma ya zo musu, ya kuma dace da abin da yake cikin Attaura da Injila na tushen addini. Kuma sun kasance kafin a saukar da shi, suna cewa,: "zamu ci nasara a kan mushirikai, kuma za a yi mana buxi lokacin da aka aiko da wani Annabi, mu yi imani da shi, mu bi shi. A lokacin da Alqur'ani da Annabi Muhammad (S.A.W) suka zo akan siffar da suka sani, da gaskiyar da suka sani, sai suka kafirce masa. La'antar Allah da tabbata a kan waxanda suka kafirce wa Allah da Manzonsa.**

**90** **Tir da waxanda suka canza rabonsu na imani da Allah da Manzanninsa, suka kafircewa abin da Allah ya saukar, suka qaryata Manzanninsa, don zalunci da hasada, saboda an ba Annabi Muhammad (S.A.W) Annabta da Alqur'ani, don haka suka cancanci fushi daga Allah, saboda kafirce wa Annabi Muhammad (S.A.W) da canza Attaura da suka yi. Waxanda suka kafirta da Annabcin Annabi Muhammad (S.A.W) suna da azaba ta qasqanci ranar Alqiyama.**

**91** **Idan aka ce da waxannan Yahudawa: Ku yi imani da abin da Allah ya saukar ga Manzonsa na gaskiya da shiriya, sai su ce,: "Muna imani da abin da aka saukar ga Annabawanmu", amma suna kafirce wa abin da ba shi ba, na daga abin da aka saukar wa Muhammad (S.A.W). Ga shi kuwa wannan Alqur'ani shi ne gaskiya, kuma ya dace da abin da yake wajensu daga Allah, don haka da sun yi imanin gaskiya da abin da aka saukar musu, da sun zama sun yi imani da wannan Alqur'ani kenan. Ka ce da su - ya kai wannan Annabi - kana mai ba su amsa,: "Don me a da, kuke kashe Annabawan Allah in dai kun yi imani da gaske da abin da suka zo muku da shi na gaskiya?!.**

**92** **Manzonku Annabi Musa (A.S) ya zo muku da ayoyi bayyanannu, waxanda suke nuna gaskiyarsa, amma sai kuka sanya xan maraqi ya zama Allanku, kuna bauta masa, a lokacin da Annabi Musa ya tafi wurin gamuwa da Ubangijinsa. Kuka zama azzalumai saboda shirkar da kuka yi da Allah, alhali shi ne wanda ya cancanta a bauta masa, shi kaxai, ba waninsa ba.**

**93** **Ku tuna lokacin da muka yi alqawari mai qarfi da ku, a kan zaku bi Annabi Musa (A.S), kuma zaku karvi abin da ya zo da shi daga wajen Allah. Muka xaukaka dutse a samanku don tsoratar da ku, muka ce da ku: "Ku riqi abin da muka baku na Attaura da kyau, ku saurari abin da ya zo da shi, sauraro na karva, in kuma baku yi haka ba kuwa, za mu sako muku dutsen a kanku", sai kuka ce,: "Mun ji da kunnuwanmu, amma mun sava da ayyukanmu". Bautar xan maraqi ya tabbata a zukatansu saboda kafircinsu. Ka ce da su - Ya kai wannan Annabi -: "Tir da abin da imaninku yake umartarku da shi na kafirce wa Allah in dai ku muminai ne, saboda imani na gaskiya ba kafirci tare da shi".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yahudawa sun fi dukkan mutane hassada, saboda hassadarsu ta kai su zuwa ga kafircewa Allah, da mayar da abin da ya saukar, kawai don Manzon Allah bai zama daga cikinsu ba.**

**2 - Imani na gaskiya yana wajabta wa mai shi, yarda da duk abin da aka saukar na littafai, da dukkan waxanda aka aiko na Manzanni.**

**3 - Warware alqawari yana cikin al'adar Yahudawa, kuma wannan ne halinsu har zuwa yau.**

قُلْ إِن كَانَتْ لَكُمُ الدَّارُ الْآخِرَةُ عِندَ اللَّهِ خَالِصَةً مِّن
دُونِ النَّاسِ فَتَمَنَّوُا الْمَوْتَ إِن كُنتُمْ صَادِقِينَ ﴿٩٤﴾ وَلَن
يَتَمَنَّوْهُ أَبَدًا بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيهِمْ ۗ وَاللَّهُ عَلِيمٌ بِالظَّالِمِينَ
﴿٩٥﴾ وَلَتَجِدَنَّهُمْ أَحْرَصَ النَّاسِ عَلَىٰ حَيَاةٍ وَمِنَ الَّذِينَ أَشْرَكُوا ۚ
يَوَدُّ أَحَدُهُمْ لَوْ يُعَمَّرُ أَلْفَ سَنَةٍ وَمَا هُوَ بِمُزَحْزِحِهِ مِنَ
الْعَذَابِ أَن يُعَمَّرَ ۗ وَاللَّهُ بَصِيرٌ بِمَا يَعْمَلُونَ ﴿٩٦﴾ قُلْ مَن
كَانَ عَدُوًّا لِّجِبْرِيلَ فَإِنَّهُ نَزَّلَهُ عَلَىٰ قَلْبِكَ بِإِذْنِ
اللَّهِ مُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ وَهُدًى وَبُشْرَىٰ لِلْمُؤْمِنِينَ
﴿٩٧﴾ مَن كَانَ عَدُوًّا لِّلَّهِ وَمَلَائِكَتِهِ وَرُسُلِهِ وَجِبْرِيلَ
وَمِيكَالَ فَإِنَّ اللَّهَ عَدُوٌّ لِّلْكَافِرِينَ ﴿٩٨﴾ وَلَقَدْ أَنزَلْنَا
إِلَيْكَ آيَاتٍ بَيِّنَاتٍ ۖ وَمَا يَكْفُرُ بِهَا إِلَّا الْفَاسِقُونَ ﴿٩٩﴾
أَوَكُلَّمَا عَاهَدُوا عَهْدًا نَّبَذَهُ فَرِيقٌ مِّنْهُم ۚ بَلْ أَكْثَرُهُمْ
لَا يُؤْمِنُونَ ﴿١٠٠﴾ وَلَمَّا جَاءَهُمْ رَسُولٌ مِّنْ عِندِ اللَّهِ مُصَدِّقٌ
لِّمَا مَعَهُمْ نَبَذَ فَرِيقٌ مِّنَ الَّذِينَ أُوتُوا الْكِتَابَ
كِتَابَ اللَّهِ وَرَاءَ ظُهُورِهِمْ كَأَنَّهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ﴿١٠١﴾



**(94) Ka ce – Ya kai wannan Annabi – Idan dai gidan Aljannah naku ne ku kaxai Yahudawa a lahira, ba wanda zai shige ta daga cikin mutane, to ku yi burin mutuwa, ku neme ta, don ku same ta da sauri, ku huta da wahalar rayuwar duniya da damuwarta, ku yi hakan, indai abin da kuke da'awa gaskiya ne.**

**(95) Ba za su tava burin mutuwa ba har abada, saboda da abin da suka gabatar na kafirce wa Allah a rayuwarsu, da qaryata Manzanninsa, da canza littafansa. Allah yana sane da azzalumai da wasunsu, kuma zai sakawa kowa da abin da ya aikata.**

**(96) Za ka sami Yahudawa – Ya kai wannan Annabi – sun fi kowa kwaxayin rayuwa duk da qasqanci da wulaqancin da yake cikinta, kai! sun fi Mushirikai waxanda ba su yi imani da tashin alqiyama da hisabi ba kwaxayin rayuwa, alhali ga su ma'abota littafi ne, sun yi imani da tashi bayan mutuwa da hisabi. Amma za ka sami mutum a cikinsu yana so a rayuwarsa ya kai shekaru dubu, kuma koda wannan daxewar a rayuwar ba zata nisantar shi daga azabar Allah ba,. Allah yana ganin ayyukansu, babu abin da yake vuya a gare shi, kuma zai saka musu.**

**(97) Ya kai wannan Annabi – ka cewa bayahuden nan da ya ce, "Mu Jibrilu maqiyinmu ne a cikin Mala'iku" ka ce da shi, "duk wanda ya zama maqiyin Jibrilu, to ya sani, Jibrilu shi ne ya saukar da Alqur'ani a zuciyarka da izinin Allah, yana mai gasgata abin ya gabata na littafan Allah, kamar Attaura da Injila, kuma yana nuna alheri, da bushara ga muminai da abin da Allah ya tanadar musu na ni'ima. To duk wanda yake gaba da wanda wannan ce siffar shi, to yana cikin vatattu.**

**(98) Wanda ya zama maqiyin Allah da Mala'ikunsa da Manzanninsa, kuma maqiyin mala'ikun nan makusanta guda biyu, Jibrilu da Mikala, to ya sani Allah maqiyin dukkan kafirai ne, duk kuwa wanda Allah yake qi to ya tave, ya yi hasara bayyananniya.**

**(99) Ya kai wannan Annabi, mun saukar maka da ayoyi bayyanannu, waxanda suke nuna gaskiyarka cikin abin da ka zo da shi na annabta da wahayi. Ba wanda yake kafirce musu bayan bayyanarsu da fitowarsu fili sai waxanda suke fita daga addinin Allah.**

**(100) Saboda munanan halayen Yahudawa duk lokacin da suka xauki alqawari da kansu – daga ciki akwai alqawarin za su yi imani da abin da Attaura ta nuna na annabcin Annabi Muhammad (S.A.W) – sai wasu daga cikinsu sun warware shi. Kai! Mafi yawancin waxannan Yahudawa ba su yi imani da haqiqanin abin da Allah ya saukar ba, saboda imani yana sa a cika alqawari.**

**(101) Yayin da Annabi Muhammad (S.A.W) Manzo daga Allah ya zo musu da abin da ya dace da abin da yake cikin Attaura na siffarsa, sai wasu vangare suka bijirewa abin da Attaura ta nuna, suka jefar da ita a bayansu, suka yi watsi da ita, ba su damu ba, suka yi daidai da jahilin da baya amfanuwa da abin da yake cikinta na shiriya da gaskiya, don haka bai damu da ita ba.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Mumini na gaskiya shi ne wanda yake fatan abin da yake wajen Allah na ni'ima dauwamammiya, don haka yake farin ciki da gamuwa da Allah, kuma baya tsoron mutuwa.**

**2 - Kwaxayin Yahudawa na rayuwa a duniya, koda kuwa rayuwar qasqanci ce da wulaqanci.**

**3 - Duk wanda ya yi gaba da waliyyan Allah makusanta, to ya yi gaba da Allah Maxaukakin Sarki**

**4 - Bijirewar Yahudawa daga annabtar Manzon Allah (S.A.W) bayan sun san gaskiyarsa daga abin da yake hannunsu na littafai. 5 - Duk wanda bai amfanu da iliminsa ba, to ya yi daidai a siffata shi da jahilci, saboda ya yi kama da jahili a cikin jahilcinsa.**

وَٱتَّبَعُواْ مَا تَتۡلُواْ ٱلشَّيَٰطِينُ عَلَىٰ مُلۡكِ سُلَيۡمَٰنَۖ وَمَا كَفَرَ
سُلَيۡمَٰنُ وَلَٰكِنَّ ٱلشَّيَٰطِينَ كَفَرُواْ يُعَلِّمُونَ ٱلنَّاسَ
ٱلسِّحۡرَ وَمَآ أُنزِلَ عَلَى ٱلۡمَلَكَيۡنِ بِبَابِلَ هَٰرُوتَ وَمَٰرُوتَۚ
وَمَا يُعَلِّمَانِ مِنۡ أَحَدٍ حَتَّىٰ يَقُولَآ إِنَّمَا نَحۡنُ فِتۡنَةٞ فَلَا
تَكۡفُرۡۖ فَيَتَعَلَّمُونَ مِنۡهُمَا مَا يُفَرِّقُونَ بِهِۦ بَيۡنَ ٱلۡمَرۡءِ
وَزَوۡجِهِۦۚ وَمَا هُم بِضَآرِّينَ بِهِۦ مِنۡ أَحَدٍ إِلَّا بِإِذۡنِ ٱللَّهِۚ
وَيَتَعَلَّمُونَ مَا يَضُرُّهُمۡ وَلَا يَنفَعُهُمۡۚ وَلَقَدۡ عَلِمُواْ لَمَنِ
ٱشۡتَرَىٰهُ مَا لَهُۥ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ مِنۡ خَلَٰقٖۚ وَلَبِئۡسَ مَا شَرَوۡاْ بِهِۦٓ
أَنفُسَهُمۡۚ لَوۡ كَانُواْ يَعۡلَمُونَ ١٠٢ وَلَوۡ أَنَّهُمۡ ءَامَنُواْ وَٱتَّقَوۡاْ
لَمَثُوبَةٞ مِّنۡ عِندِ ٱللَّهِ خَيۡرٞۚ لَّوۡ كَانُواْ يَعۡلَمُونَ ١٠٣
يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَقُولُواْ رَٰعِنَا وَقُولُواْ ٱنظُرۡنَا
وَٱسۡمَعُواْۗ وَلِلۡكَٰفِرِينَ عَذَابٌ أَلِيمٞ ١٠٤ مَّا يَوَدُّ
ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ وَلَا ٱلۡمُشۡرِكِينَ
أَن يُنَزَّلَ عَلَيۡكُم مِّنۡ خَيۡرٖ مِّن رَّبِّكُمۡۚ وَٱللَّهُ يَخۡتَصُّ
بِرَحۡمَتِهِۦ مَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ ذُو ٱلۡفَضۡلِ ٱلۡعَظِيمِ ١٠٥



**(102) Yayin da suka bar addinin Allah, sai suka canza shi da bin abin da Shaixanu suke faxa na qarya a kan mulkin Annabin Allah Sulaiman (A.S). A yayin da suka riya cewa mulkinsa ya tabbata ne da sihiri. To Annabi Sulaimanu (A.S) bai kafirta da yin sihiri ba – kamar yadda Yahudawa suke raya wa – su Shaixanun su ne suka kafirta, saboda suna koya wa mutane sihiri, suna koya musu sihirin da aka saukar wa Mala'ikun nan guda biyu, Haruta da Maruta a birnin Babila a qasar Iraq, don Allah ya jarrabe su, ya kuma jarrabi mutane da su. Kuma waxannan Mala'iku guda biyu basa koyawa kowa sihiri sai sun faxa masa, sun bayyana masa, sun ce, "Mu fa jarraba ce ga mutane, kada ka zama kafiri da koyon wannan sihiri". Wanda duk bai karvi wannan nasiha ba, sai ya koyi sihiri a wurinsu. Daga cikin irin sihirin da suke koya, akwai sihirin da yake raba tsakanin miji da matarsa, ta hanyar saka musu gaba a tsakaninsu. Ba wanda waxannan masu sihiri suka isa su cutar da shi, sai dai da izinin Allah da ganin damarsa. Sai su koyi abin da zai cutar da su, kuma ba zai amfane su ba. Waxannan Yahudawa sun sani cewa duk wanda ya canza littafin Allah da sihiri, baida wani rabo a lahira. Tir da abin da suka sayar da kawunansu da shi, na canza wahayin Allah da shari'arsa da sihiri. Da sun san abin da zai amfane su, da basu yi wannan vatan, da wannan mummunan aikin mabayyani ba.**

**(103) Da a ce Yahudawa sun yi imani da Allah imani na gaskiya, da sun ji tsoronsa, ta hanyar aikata abin da ya yi umarni, da barin savonsa, kuma da ladan da Allah zai ba su, ya fi abin da suke kai alheri, da sun san abin da zai amfane su.**

**(104) Allah yana fuskantar da Muminai zuwa ga zaven lafuzza masu kyau, yana cewa, "Ya waxanda suka yi imani kada ku faxi kalmar "Raa'ina" wadda take nufin, ka lura da halinmu, saboda Yahudawa suna canza wannan kalma, suna faxa wa Annabi (S.A.W) ita, amma suna nufin mummunan ma'ana da ita, ita ce "ruvewa". Don haka sai Allah ya hana wannan kalma don toshe hanyar varna, ya umarci bayinsa su riqa faxin kalmar (Unzurna) ma'ana: ka jira, mu fahimci abin da kake faxa, maimaikon waccan kalma, saboda wannan za ta bayar da ma'anar waccan ba tare da wani abun qi ba. Kafirai suna da azaba mai tsanani da raxaxi.**

**(105) Dukkan Kafirai, da mushirikai da ma'abota littafi basa son a saukar muku da wani alheri daga Ubangijinku, mai yawa ne ko kaxan. Sai dai Allah yana kevance wanda ya so daga cikin bayinsa da rahamarsa ta annabta da wahayi. Allah ma'abocin falala ne mai girma. ba wani alheri da zai samu wani sai daga gare shi, yana daga cikin falalarsa aiko Manzo da saukar da littafai.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Rashin ladabin Yahudawa, saboda sun dangana wa Annabi Sulaimanu (A.S) yin sihiri, amma Allah ya kuvutar da shi, ya karyata su.**

**2 - Sihiri yana tasiri a cikin hankali da jiki. Mai sihiri kuma kafiri ne, kisa ne hukuncinsa.**

**3 - Babu wani abu da zai faru a cikin mulkin Allah, alheri ne ko sharri, face sai Allah ya sani, kuma sai da izininsa.**

**4 - Toshe hanyar varna yana cikin manufar shari'a, don haka duk wani aiki ko magana da za su kai zuwa fahimtar wasu al'amura munana, to wajibi ne a nisance su, a yi nesa da su.**

**5 - Falala tana hannun Allah, shi ne yake kevance wanda ya so da rahamarsa da hikimarsa.**

نصف الحزب ٢

۞ مَا نَنسَخْ مِنْ ءَايَةٍ أَوْ نُنسِهَا نَأْتِ بِخَيْرٍ مِّنْهَآ أَوْ مِثْلِهَآ
أَلَمْ تَعْلَمْ أَنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ قَدِيرٌ ١٠٦ أَلَمْ تَعْلَمْ أَنَّ
ٱللَّهَ لَهُۥ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ
ٱللَّهِ مِن وَلِيٍّ وَلَا نَصِيرٍ ١٠٧ أَمْ تُرِيدُونَ أَن تَسْـَٔلُوا۟ رَسُولَكُمْ
كَمَا سُئِلَ مُوسَىٰ مِن قَبْلُ وَمَن يَتَبَدَّلِ ٱلْكُفْرَ بِٱلْإِيمَٰنِ
فَقَدْ ضَلَّ سَوَآءَ ٱلسَّبِيلِ ١٠٨ وَدَّ كَثِيرٌ مِّنْ أَهْلِ ٱلْكِتَٰبِ
لَوْ يَرُدُّونَكُم مِّنۢ بَعْدِ إِيمَٰنِكُمْ كُفَّارًا حَسَدًا
مِّنْ عِندِ أَنفُسِهِم مِّنۢ بَعْدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُمُ ٱلْحَقُّ فَٱعْفُوا۟
وَٱصْفَحُوا۟ حَتَّىٰ يَأْتِيَ ٱللَّهُ بِأَمْرِهِۦٓ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ
قَدِيرٌ ١٠٩ وَأَقِيمُوا۟ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتُوا۟ ٱلزَّكَوٰةَ وَمَا تُقَدِّمُوا۟
لِأَنفُسِكُم مِّنْ خَيْرٍ تَجِدُوهُ عِندَ ٱللَّهِ إِنَّ ٱللَّهَ بِمَا تَعْمَلُونَ
بَصِيرٌ ١١٠ وَقَالُوا۟ لَن يَدْخُلَ ٱلْجَنَّةَ إِلَّا مَن كَانَ هُودًا
أَوْ نَصَٰرَىٰ تِلْكَ أَمَانِيُّهُمْ قُلْ هَاتُوا۟ بُرْهَٰنَكُمْ إِن كُنتُمْ
صَٰدِقِينَ ١١١ بَلَىٰ مَنْ أَسْلَمَ وَجْهَهُۥ لِلَّهِ وَهُوَ مُحْسِنٌ فَلَهُۥٓ
أَجْرُهُۥ عِندَ رَبِّهِۦ وَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ١١٢



**(106) Allah Maxaukakin Sarki yana bayyana cewa yayin da yake xauke hukuncin wata aya daga Alqur'ani, ko ya xauke lafazinta ya mantar da mutane ita, to yana zuwa da abin da ya fi amfani a kusa ko a nesa, ko kuma da abin da ya yi kama da ita, saboda ilimin Allah da hikimarsa. Ka sani ya kai wannan Annabi Allah mai iko ne a kan dukkan komai, yana aikata abin da ya ga dama, yana kuma hukunta abin da ya yi nufi.**

**(107) Ka sani – Ya kai wannan Annabi – cewa Allah ne mamallakin Sammai da qassai, yana hukunta abin da ya yi nufi, ya umarci bayinsa da abin da ya ga dama, ya hana su abin da ya ga dama, ya shar'anta musu abin da ya ga dama na shari'a, ya goge abin da ya ga dama. Ba ku da wani majivinci da zai jivinci lamarinku, ko wani mataimaki da zai kare muku cuta. Allah ne kaxai majivincin wannan duka, kuma mai iko a kai.**

**(108) Ba aikinku ba ne – Yaku Muminai – ku tambayi Annabinku – tambaya ta karan-tsaye da taurin kai – kamar yadda mutanen Annabi Musa suka tambayi Annabinsu gabanin haka, kamar tambayar da suke ce, "ka nuna mana Allah qiri-qiri". Duk wanda ya canza imani da kafirci to ya vace daga barin hanya mafificiya, wato hanya madaidaiciya.**

**(109) Da yawa daga cikin Yahudu da Nasara sun yi burin su mayar da ku kafirai kuna bautawa gumaka bayan kun yi imani, saboda hassadar da take cikin zuciyarsu. Suna muku burin haka ne, bayan ya bayyana gare su abin da Annabi (S.A.W) ya zo da shi gaskiya ne. don haka ku yi afuwa ya ku Muminai, ku kawar da kai daga jahilcinsu da mummunan abin da yake zuciyarsu, har hukuncin Allah ya zo. Haqiqa hukuncin Allah da lamarinsa ya zo a kansu, an wayi gari ana ba wa kafiri zavi, ko dai musulunci ko ya bayar da jizya, ko kuma a yaqe shi. Haqiqa Allah mai iko ne akan dukkan komai, ba zaku gagare shi ba.**
**Bayan haka sai Allah ya umarci muminai da haquri akan cutar su da ake yi, da tabbata a kan addini, da qarfafa imaninsu. Ya ce,:**

**(110) Ku yi sallah cikakkiya da rukunanta da wajibanta da sunnoninta. Ku fitar da zakkah zuwa ga waxanda suka cancanceta. Duk wani aiki nagari da za ku yi a rayuwarku, ku gabatar da shi kafin mutuwarku, don ya zama tanadi gare ku, kuma zaku samu ladansa a wajen Ubangijinku ranar alqiyama, ya saka muku da abin da kuka aikata. Haqiqa Allah yana ganin abin da kuke aikatawa, kuma zai sakawa kowa da abin da ya aikata.**

**(111) Kowane vangare cikin Yahudawa da Nasara sun ce Aljannah ta su ce. Yahudawa suka ce, "ba wanda zai shige ta sai wanda yake Bayahude". Nasara suka ce, "Ba wanda zai shiga Aljannah sai wanda yake Banasare". Wannan duk burace-buracensu ne na wofi. Ka faxa musu - Ya kai wannan Annabi - kana mai musu raddi, ka ce, "ku kawo hujjarku akan abin da kuke zato in dai tabbas kuna da gaskiya cikin abin da kuke da'awa".**

**(112) Wanda kaxai zai shiga Aljannah shi ne wanda ya tsarkake zuciyarsa ga Allah, ya fuskance shi, yana mai kyautata wa a cikin ibadarsa, da bin abin da Manzon Allah ya zo da shi. Wannan shi ne wanda zai shiga Aljannah a kowace qungiya yake. Kuma ladansa yana wajen Ubangijinsa, sannan babu tsoro ga abin da suke fuskanta a lahira, kuma ba za su yi baqin ciki ba dangane da abin da ya wuce su a duniya.**
**Waxannan siffofi ba sa tabbata bayan zuwan Manzon Allah Muhammad (S.A.W) sai ga musulmai.**

## Kaxan Daga Cikin Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Dukkan lamari na Allah ne, yana canza abin da ya ga dama na daga hukunce-hukuncensa da shari'arsa, ya bar abin da ya ga dama, kuma duk hakan yana faruwa da saninsa da hikimarsa.**

**2 - Hassadar da yawa daga cikin ma'abota littafi ga wannan al'umma, saboda abin da Allah ya keve ta da shi na imani da bin Manzon Allah (S.A.W), har suke mata burin ina ma ta dawo kafirci kamar yadda take da can.**

وَقَالَتِ ٱلۡيَهُودُ لَيۡسَتِ ٱلنَّصَٰرَىٰ عَلَىٰ شَيۡءٖ وَقَالَتِ ٱلنَّصَٰرَىٰ
لَيۡسَتِ ٱلۡيَهُودُ عَلَىٰ شَيۡءٖ وَهُمۡ يَتۡلُونَ ٱلۡكِتَٰبَۗ كَذَٰلِكَ
قَالَ ٱلَّذِينَ لَا يَعۡلَمُونَ مِثۡلَ قَوۡلِهِمۡۚ فَٱللَّهُ يَحۡكُمُ بَيۡنَهُمۡ
يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ فِيمَا كَانُواْ فِيهِ يَخۡتَلِفُونَ ١١٣ وَمَنۡ أَظۡلَمُ مِمَّن
مَّنَعَ مَسَٰجِدَ ٱللَّهِ أَن يُذۡكَرَ فِيهَا ٱسۡمُهُۥ وَسَعَىٰ فِي خَرَابِهَآۚ
أُوْلَٰٓئِكَ مَا كَانَ لَهُمۡ أَن يَدۡخُلُوهَآ إِلَّا خَآئِفِينَۚ لَهُمۡ فِي
ٱلدُّنۡيَا خِزۡيٞ وَلَهُمۡ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ عَذَابٌ عَظِيمٞ ١١٤ وَلِلَّهِ ٱلۡمَشۡرِقُ
وَٱلۡمَغۡرِبُۚ فَأَيۡنَمَا تُوَلُّواْ فَثَمَّ وَجۡهُ ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ وَٰسِعٌ عَلِيمٞ ١١٥
وَقَالُواْ ٱتَّخَذَ ٱللَّهُ وَلَدٗاۗ سُبۡحَٰنَهُۥۖ بَل لَّهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلۡأَرۡضِۖ كُلّٞ لَّهُۥ قَٰنِتُونَ ١١٦ بَدِيعُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ
وَإِذَا قَضَىٰٓ أَمۡرٗا فَإِنَّمَا يَقُولُ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ١١٧ وَقَالَ
ٱلَّذِينَ لَا يَعۡلَمُونَ لَوۡلَا يُكَلِّمُنَا ٱللَّهُ أَوۡ تَأۡتِينَآ ءَايَةٞۗ
كَذَٰلِكَ قَالَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِم مِّثۡلَ قَوۡلِهِمۡۘ تَشَٰبَهَتۡ
قُلُوبُهُمۡۗ قَدۡ بَيَّنَّا ٱلۡأٓيَٰتِ لِقَوۡمٖ يُوقِنُونَ ١١٨ إِنَّآ أَرۡسَلۡنَٰكَ
بِٱلۡحَقِّ بَشِيرٗا وَنَذِيرٗاۖ وَلَا تُسۡـَٔلُ عَنۡ أَصۡحَٰبِ ٱلۡجَحِيمِ ١١٩



**(113) Yahudawa suka ce, “Nasara basa kan addini ingantacce”. Nasara suka ce, “Yahudu basa kan wani addini ingantacce”. Dukkaninsu suna karanta littafan da Allah ya saukar musu, da abin da yake cikinsu na umarni da imani da dukkan Annabawa babu wani bambanci. A cikin wannan aiki na su sun yi kama da waxanda basu da ilimi daga cikin Mushirikai, yayin da suka qaryata Manzanni gaba xayansu, da dukkan abin da Allah ya saukar na littafai. Don haka Allah zai yi hukunci tsakanin masu savani gaba xayansu ranar alqiyama, da hukuncinsa na adalci wanda ya ba bayinsa labari, na cewa babu rabo sai da imani da dukkan abin da Allah ya saukar.**

**(114) Babu wanda ya fi zalunci irin wanda ya hana a ambaci sunan Allah a Masallatansa, ya hana sallah da zikiri da karatun Alqur’ani. Ya yi ta qoqarin rushe su da varna a cikinsu, ta hanyar ruguza su da hana yin ibada a cikinsu. Waxannan masu varna a cikinsu babu abin da ya dace da su face su shiga waxannan masallatai na Allah suna masu tsoronsa, zukatansu suna raurawa, saboda abin da suke kai na kafirci da kange mutane daga Masallatan Allah. A duniya suna da qasqanci da wulaqanci a hannun muminai, a lahira kuma suna da azaba mai girma akan hana mutane shiga masallaci.**

**(115) Mahudar rana da inda take faxuwa da abin da yake tsakaninsu duka na Allah ne. yana umartar bayinsa da abin da ya so, don haka duk inda kuka fuskanta, to kuna fuskantar Allah ne. saboda haka idan ya umarce ku da fuskantar Baitul Muqaddas ko Ka’abah, ko kuka yi kuskuren fuskantar alqibla ko hakan ya yi muku wahala, to ba komai a kanku, saboda dukkan vangarori na Allah ne. Haqiqa Allah mai yalwa ne, yana yalwata wa bayi da rangwamensa da rahamarsa. Ya san dukkan niyyoyinsu da ayyukansu.**

**(116) Yahudawa da Nasara da Mushirikai suka ce, “Allah yana da xa”. Tsarki ya tabbata ga Allah, Shi Mawadaci ne ga barin bayinsa, wanda yake buqatar xa shi yake riqonsa. Shi kuwa Allah Shi yake da mulkin Sammai da qassai, dukkan bayi halittansa ne, tsarki ya tabbata a gare shi, masu qasqantar da kai ne gare shi, yana sarrafa su da abin da ya ga dama.**

**(117) Allah ne ya qirqiri sammai da qassai ba tare da ya ga misalinsu a wurin wani ba. Idan ya qaddara wani lamari ya yi nufin faruwarsa, kawai zai cewa wannan lamari ne “Kasance” sai ya kasance kamar yadda Allah ya so ya kasance, babu mai mayar da umarnin Allah da hukuncinsa.**

**(118) Waxanda ba su sani ba daga cikin Mushirikai da Ma’abota littafi suka ce, suna masu taurin kai, da qin gaskiya “Don me Allah ba zai magana da mu ba babu wani tsakani, mu da shi, ko kuma mu ga wata alama da ta kevanta da mu, mu kaxai?”. Irin wannan magana ita ce al’ummun da suka gabata waxanda suka qaryata Manzanni suka faxa wa Manzanninsu, duk da kuwa sun sava a zamani da wurare. Haqiqa mun bayyana ayoyi ga mutanen da suka sakankance da gaskiya idan ta bayyana a gare su, ba sa shakka, kuma taurin kai ba ya hana su.**

**(119) Haqiqa mun aiko ka – Ya kai wannan Annabi – da addinin gaskiya wanda babu shakka a cikinsa, saboda ka yi wa Muminai bushara da Aljannah, ka gargaxi kafirai daga Wuta. Babu abin da yake kanka sai isar da saqo, isarwa mabayyaniya. Allah ba zai tambaye ka waxanda ba su yi imani da kai ba, daga cikin yan wutar Jahimu.**

## Kaxan Daga Cikin Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Kafirci abu xaya ne, ko da kuwa masu yin sa sun sava a jinsi da wuraren zama. Suna yin kama a cikin kafircinsu da maganganunsu a kan Allah ba da ilimi ba. 2 - Wanda ya fi kowa girman laifi da zunubi a cikin mutane, shi ne wanda yake kare mutane daga hanyar Allah, ko ya hana wanda ya yi nufin aikin alheri aikatawa. 3 - Allah ya tsarkaka daga barin Mata da xa. Tsarki ya tabbata a gare shi, baya buqatar wani abu daga halittarsa.**

وَلَن تَرۡضَىٰ عَنكَ ٱلۡيَهُودُ وَلَا ٱلنَّصَٰرَىٰ حَتَّىٰ تَتَّبِعَ مِلَّتَهُمۡۗ قُلۡ
إِنَّ هُدَى ٱللَّهِ هُوَ ٱلۡهُدَىٰۗ وَلَئِنِ ٱتَّبَعۡتَ أَهۡوَآءَهُم بَعۡدَ ٱلَّذِي
جَآءَكَ مِنَ ٱلۡعِلۡمِ مَا لَكَ مِنَ ٱللَّهِ مِن وَلِيّٖ وَلَا نَصِيرٍ ١٢٠ ٱلَّذِينَ
ءَاتَيۡنَٰهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ يَتۡلُونَهُۥ حَقَّ تِلَاوَتِهِۦٓ أُوْلَٰٓئِكَ يُؤۡمِنُونَ بِهِۦۗ وَمَن
يَكۡفُرۡ بِهِۦ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ١٢١ يَٰبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٱذۡكُرُواْ نِعۡمَتِيَ
ٱلَّتِيٓ أَنۡعَمۡتُ عَلَيۡكُمۡ وَأَنِّي فَضَّلۡتُكُمۡ عَلَى ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٢٢ وَٱتَّقُواْ يَوۡمٗا
لَّا تَجۡزِي نَفۡسٌ عَن نَّفۡسٖ شَيۡـٔٗا وَلَا يُقۡبَلُ مِنۡهَا عَدۡلٞ وَلَا تَنفَعُهَا
ثلاثة أرباع الحزب ٢ شَفَٰعَةٞ وَلَا هُمۡ يُنصَرُونَ ١٢٣ ۞ وَإِذِ ٱبۡتَلَىٰٓ إِبۡرَٰهِـۧمَ رَبُّهُۥ بِكَلِمَٰتٖ
فَأَتَمَّهُنَّۖ قَالَ إِنِّي جَاعِلُكَ لِلنَّاسِ إِمَامٗاۖ قَالَ وَمِن ذُرِّيَّتِيۖ قَالَ
لَا يَنَالُ عَهۡدِي ٱلظَّٰلِمِينَ ١٢٤ وَإِذۡ جَعَلۡنَا ٱلۡبَيۡتَ مَثَابَةٗ لِّلنَّاسِ
وَأَمۡنٗا وَٱتَّخِذُواْ مِن مَّقَامِ إِبۡرَٰهِـۧمَ مُصَلّٗىۖ وَعَهِدۡنَآ إِلَىٰٓ إِبۡرَٰهِـۧمَ
وَإِسۡمَٰعِيلَ أَن طَهِّرَا بَيۡتِيَ لِلطَّآئِفِينَ وَٱلۡعَٰكِفِينَ وَٱلرُّكَّعِ ٱلسُّجُودِ
١٢٥ وَإِذۡ قَالَ إِبۡرَٰهِـۧمُ رَبِّ ٱجۡعَلۡ هَٰذَا بَلَدًا ءَامِنٗا وَٱرۡزُقۡ أَهۡلَهُۥ
مِنَ ٱلثَّمَرَٰتِ مَنۡ ءَامَنَ مِنۡهُم بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِۚ قَالَ وَمَن كَفَرَ
فَأُمَتِّعُهُۥ قَلِيلٗا ثُمَّ أَضۡطَرُّهُۥٓ إِلَىٰ عَذَابِ ٱلنَّارِۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمَصِيرُ ١٢٦



**(120) Allah yana magana da Annabinsa, yana mai masa gargaxi da tsoratarwa, ya ce masa, "Yahudawa da Nasara baza su tava yarda da kai ba, har sai ka bar Musulunci, ka bi abin da suke kai". Idan kuwa haka ya faru daga wajenka, ko daga wajen wani mabiyinka, bayan abin da ya zo maka na gaskiya bayyananniya, to ba za ka samu wani mataimaki daga wajen Allah ba. Wannan bayani ne na haxarin barin gaskiya da bin mavarnata.**

**(121) Alqur'ani mai girma yana magana ne akan wasu daga cikin ma'abota littafi, waxanda suke aiki da littafan da suke hannunsu, suke bin su da gaskiya. Waxannan suna samun alamomin da suke nuna gaskiyar Annabi Muhammad (S.A.W) a littafansu, don haka suke gaggawar imani da shi. Wasu kuma sai su ci gaba da kafircinsu. Asara ta tabbata a gare su.**

**(122) Yaku bani-Isra'ila ku tuna ni'imata ta addini da ta duniya da nai muku. Ku tuna cewa na fifita ku da baku annabci da mulki a kan sauran mutanen zamaninku.**

**(123) Ku sanya shamaki tsakaninku da azabar Allah, ta hanyar bin umarnin Allah da nisantar abubuwan da ya hana, saboda a wannan ranar wata rai bata wadatar da wata rai da wani abu, kuma baza a karvi fansa daga gare ta ba, komai girman abin da za ta bayar xin, haka kuma ba ceton da zai amfane ta, ko ceton waye kuwa, duk girmansa, sannan kuma bata da wani mataimaki da zai taimake ta komai bayan Allah Maxaukakin Sarki.**

**(124) Ku tuna lokacin da Allah ya jarraba Annabi Ibrahim, da abin da ya umarce shi na hukunce-hukunce, da nauyin da ya xora masa. Kuma Annabi Ibrahim ya aikata su kamar yadda ake so. Sai Allah ya cewa masa: "Na sanya ka abin koyi ga mutane, su yi koyi da ayyukanka da halayenka". Sai Annabi Ibrahim ya ce, "Ya Allah ka sanya hakan ma a cikin zurriyata, suma su zama jagorori ababen koyi ga mutane". Sai Allah ya amsa masa da cewa: "Ai azzalumai daga cikin zurriyarka ba sa samun alqawarin jagoranci a addini a wurina".**

**(125) Ka tuna yayin da muka sanya xaki mai alfarma ya zama wurin komawar mutane, zukatansu sun ratayu da shi, duk lokacin da suka tafi daga wajensa sai sun dawo wurinsa. Ya sanya shi aminci gare su, ba a musu ta'addanci a cikinsa. kuma ya ce da mutane: "Ku riqi dutsen da Annabi Ibrahim yake tsayawa a kansa, a lokacin yana gina Ka'abah, ku riqe shi ya zama wurin sallah a gare ku. Muka yi wasiyya ga Annabi Ibrahim da xansa Annabi Isma'ila akan su tsarkake xakin nan mai alfarma daga qazanta, da gumaka, su shirya shi ga duk wanda yake son ibadar xawafi ko i'itikafi, ko sallah, ko waninta a cikinsa.**

**(126) Ka tuna ya kai wannan Annabi yayin da Annabi Ibrahim yake kiran Ubangijinsa, yana cewa, "Allah ka sanya garin Makkah ya zama amintacce, ba a cutar da wani a cikinsa, ka azurta mazaunansa da kayan marmari kala-kala, ka keve waxanda suka yi imani da kai da wannan arziqi har zuwa ranar alqiyama" Sai Allah ya ce, "Wanda duk ya kafirce a cikinsu, zan jiyar da shi daxi kaxan a duniya, sannan a lahira in sanya shi da qarfi cikin azabar wuta". Tir da makomar da zasu koma cikinta ranar alqiyama.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Duk abin da musulmai za su yi wa Yahudawa da Nasara na alheri, ba za su yarda da su ba, har sai sun fitar da su daga addinininsu, sun bi su a kan vatan da suke kai.**

**2 - Ba a samun jagoranci a addini sai da kyakkyawan yaqini da haquri wajen aikata umarnin Allah.**

**3 - Albarkar addu'ar Annabi Ibrahim ga gari mai alfarma (Wato Makkah), ta yadda ya sanya shi wuri ne mai aminci ga mutane, kuma ya fifita mazauna wannan gari da arziqi kala-kala.**

وَإِذۡ يَرۡفَعُ إِبۡرَٰهِـۧمُ ٱلۡقَوَاعِدَ مِنَ ٱلۡبَيۡتِ وَإِسۡمَٰعِيلُ رَبَّنَا تَقَبَّلۡ
مِنَّآۖ إِنَّكَ أَنتَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ١٢٧ رَبَّنَا وَٱجۡعَلۡنَا مُسۡلِمَيۡنِ
لَكَ وَمِن ذُرِّيَّتِنَآ أُمَّةٗ مُّسۡلِمَةٗ لَّكَ وَأَرِنَا مَنَاسِكَنَا وَتُبۡ عَلَيۡنَآۖ
إِنَّكَ أَنتَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ١٢٨ رَبَّنَا وَٱبۡعَثۡ فِيهِمۡ رَسُولٗا مِّنۡهُمۡ
يَتۡلُواْ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتِكَ وَيُعَلِّمُهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحِكۡمَةَ
وَيُزَكِّيهِمۡۖ إِنَّكَ أَنتَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ١٢٩ وَمَن يَرۡغَبُ عَن مِّلَّةِ
إِبۡرَٰهِـۧمَ إِلَّا مَن سَفِهَ نَفۡسَهُۥۚ وَلَقَدِ ٱصۡطَفَيۡنَٰهُ فِي ٱلدُّنۡيَاۖ
وَإِنَّهُۥ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ لَمِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ١٣٠ إِذۡ قَالَ لَهُۥ رَبُّهُۥٓ أَسۡلِمۡۖ
قَالَ أَسۡلَمۡتُ لِرَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٣١ وَوَصَّىٰ بِهَآ إِبۡرَٰهِـۧمُ بَنِيهِ
وَيَعۡقُوبُ يَٰبَنِيَّ إِنَّ ٱللَّهَ ٱصۡطَفَىٰ لَكُمُ ٱلدِّينَ فَلَا تَمُوتُنَّ
إِلَّا وَأَنتُم مُّسۡلِمُونَ ١٣٢ أَمۡ كُنتُمۡ شُهَدَآءَ إِذۡ حَضَرَ يَعۡقُوبَ
ٱلۡمَوۡتُ إِذۡ قَالَ لِبَنِيهِ مَا تَعۡبُدُونَ مِنۢ بَعۡدِيۖ قَالُواْ نَعۡبُدُ
إِلَٰهَكَ وَإِلَٰهَ ءَابَآئِكَ إِبۡرَٰهِـۧمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِسۡحَٰقَ إِلَٰهٗا
وَٰحِدٗا وَنَحۡنُ لَهُۥ مُسۡلِمُونَ ١٣٣ تِلۡكَ أُمَّةٞ قَدۡ خَلَتۡۖ لَهَا مَا كَسَبَتۡ
وَلَكُم مَّا كَسَبۡتُمۡۖ وَلَا تُسۡـَٔلُونَ عَمَّا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٣٤



**(127) Ka tuna ya kai wannan Annabi lokacin da Annabi Ibrahim da Annabi Isama'il suka assasa Ka'abah, suna cewa – cikin qanqan da kai -: "Ya ubangijinmu ka karvi ayyukanmu – wanda daga cikinsu akwai gina wannan xaki – Haqiqa Kai mai amsa addu'a ne, kuma masanin niyyoyinmu da ayyukanmu".**

**(128) Ya Ubangjinmu ka sanya mu masu miqa wuya ga lamarinka, masu qanqan da kai gareka, bama haxa wani da kai a cikin ibada, ka sanya daga cikin zurriyarmu a samu wata al'umma mai miqa wuya gare ka. Ka sanar da mu yadda ake bauta maka, ka yafe mana zunubanmu da gazawarmu wajen yi maka xa'a. Haqiqa Kai mai yawan karvar tuba ne ga wanda ya tuba daga cikin bayinka, kuma mai jinqansu ne.**

**(129) Ya Allah ka aiko musu da Manzo daga zurriyar Annabi Isma'il. Yana karanta musu ayoyinka waxanda aka saukar, yana koya musu Alqur'ani da Sunnah, yana tsakake su daga shirka da munanan abubuwa. Haqiqa Kai ne mai qarfi mai rinjaye, mai hikima cikin ayyukanka da hukunce-hukuncenka.**

**(130) Ba wanda yake barin addinin Annabi Ibrahim (A.S) zuwa wani addini daga cikin addinai, sai wanda ya zalunci kansa da wauta da mummunan tsari, na barin gaskiya zuwa ga qarya. Sai wanda ya yardarwa kansa wulaqanci. Mun zavi Annabi Ibrahim ya zama Manzo, kuma Badaxayi a duniya. A lahira kuma yana cikin salihai, waxanda suka sauke abin da Allah ya wajabta musu, suka samu manyan matsayi.**

**(131) Allah ya zave shi saboda gaggawarsa zuwa ga musulunci, yayin da Ubangijinsa ya ce masa "Ka tsarkake ibada gare ni, ka qanqan da kanka zuwa gare ni da xa'a" sai ya amsa wa Ubangijinsa ya ce "Na miqa wuya zuwa ga Allah, Mahalincin bayi, mai azurta su, mai tsara al'amuransu.**

**(132) Annabi Ibrahim ya yi wa ya'yansa wasiyya da wannan kalma, ita ce faxinsa "Na miqa wuya ga Ubangijin Talikai". Hakanan Annabi Yaqub ya yi wa 'yayansa wasiyya da wannan kalma, su duka biyun suka cewa 'ya'yansu,: "Haqiqa Allah ya zavar muku addinin musulunci, ku yi riqo da shi har mutuwa ta zo muku, kuna masu miqa wuya ga Allah a zahiri da baxini".**

**(133) Ko kuna nan lokacin da mutuwa ta zo wa Annabi Yaqub, yayin da ya cewa ya'yansa, yana tambayarsu, "Me zaku bautawa bayan mutuwata? Sai suka ba shi amsar tambayarsa, suka ce, "Muna bautawa abin bautawarka, abin bautawar Annabi Ibrahim da Annabi Isma'il da Annabi Ishaq, abin bautawa guda xaya, ba shi da abokin tarayya, shi kaxai mu, muka miqa wa wuya.**

**(134) Wannan al'umma ce da ta wuce a cikin al'ummun da suka wuce, ta tafi zuwa ga abin da ta gabatar na ayyuka, abin da ta yi mai kyau tana da ladansa, ku ma kuna da ladan abin da kuka yi, ba za a tambaye ku ayyukansu ba, ba za a kama wani da zunubin wani ba, kowa za a saka masa ne da abin da ya gabatar, don haka kada ayyukan waxanda suka gabata ya shagaltar da ku ga barin duba ayyukanku, babu abin da zai amfani xayanku bayan rahamar Allah sai aikinsa na qwarai.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Mumini mai tsoron Allah baya ruxuwa da ayyukansa na qwarai, yana tsoron kada a dawo masa da ayyukansa, a qi karva, don haka yake yawaita roqon Allah da ya karvi ayyukansa. 2 - Albarkar addu'ar baban Annabawa Annabi Ibrahim (A.S) ta inda Allah ya amsa addu'arsa, ya sa cikamakin Annabawa, mafificinsu daga cikin mutanen Makkah. 3 - Addinin Annabi Ibrahim (A.S) shi ne addinin gaskiya da ya dace da xabi'ar halittar mutum. Ba wanda yake qin wannan addini, yake gudunsa sai jahili, wanda ya savawa xabi'arsa da aka halicce shi a kanta. 4 - Shar'anta yin wasiyya ga zurriya da su bi shiriya, da yin alqawari da su a kan riqo da gaskiya da tabbata a kanta.**

وَقَالُواْ كُونُواْ هُودًا أَوۡ نَصَٰرَىٰ تَهۡتَدُواْۗ قُلۡ بَلۡ مِلَّةَ إِبۡرَٰهِـۧمَ
حَنِيفٗاۖ وَمَا كَانَ مِنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ١٣٥ قُولُوٓاْ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَمَآ
أُنزِلَ إِلَيۡنَا وَمَآ أُنزِلَ إِلَىٰٓ إِبۡرَٰهِـۧمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَ
وَٱلۡأَسۡبَاطِ وَمَآ أُوتِيَ مُوسَىٰ وَعِيسَىٰ وَمَآ أُوتِيَ ٱلنَّبِيُّونَ مِن
رَّبِّهِمۡ لَا نُفَرِّقُ بَيۡنَ أَحَدٖ مِّنۡهُمۡ وَنَحۡنُ لَهُۥ مُسۡلِمُونَ ١٣٦
فَإِنۡ ءَامَنُواْ بِمِثۡلِ مَآ ءَامَنتُم بِهِۦ فَقَدِ ٱهۡتَدَواْۖ وَّإِن تَوَلَّوۡاْ
فَإِنَّمَا هُمۡ فِي شِقَاقٖۖ فَسَيَكۡفِيكَهُمُ ٱللَّهُۚ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ
١٣٧ صِبۡغَةَ ٱللَّهِ وَمَنۡ أَحۡسَنُ مِنَ ٱللَّهِ صِبۡغَةٗۖ وَنَحۡنُ لَهُۥ
عَٰبِدُونَ ١٣٨ قُلۡ أَتُحَآجُّونَنَا فِي ٱللَّهِ وَهُوَ رَبُّنَا وَرَبُّكُمۡ
وَلَنَآ أَعۡمَٰلُنَا وَلَكُمۡ أَعۡمَٰلُكُمۡ وَنَحۡنُ لَهُۥ مُخۡلِصُونَ ١٣٩
أَمۡ تَقُولُونَ إِنَّ إِبۡرَٰهِـۧمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَ
وَٱلۡأَسۡبَاطَ كَانُواْ هُودًا أَوۡ نَصَٰرَىٰۗ قُلۡ ءَأَنتُمۡ أَعۡلَمُ أَمِ
ٱللَّهُۗ وَمَنۡ أَظۡلَمُ مِمَّن كَتَمَ شَهَٰدَةً عِندَهُۥ مِنَ ٱللَّهِۗ وَمَا ٱللَّهُ
بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعۡمَلُونَ ١٤٠ تِلۡكَ أُمَّةٞ قَدۡ خَلَتۡۖ لَهَا مَا كَسَبَتۡ
وَلَكُم مَّا كَسَبۡتُمۡۖ وَلَا تُسۡـَٔلُونَ عَمَّا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١٤١



**(135) Yahudawa suka ce wa wannan al'umma: Ku zama yahudawa sai ku kasance a kan shiriya. Nasara suka ce, "Ku zama nasara sai ku kasance akan shiriya" to ka ce musu – ya kai wannan Annabi – kaba su amsa ka ce, "A'a mu zamu bi addinin Annabi Ibrahim ne, wanda yake karkata ga barin addinin qarya zuwa ga addinin gaskiya, bai zama cikin waxanda suka haxa Allah da wani ba a wajen bauta". (136) Ku ce – Ya ku Muminai – ga waxannan masu da'awar qaryar daga Yahudawa da Nasara, mun yi imani da Allah da Alqur'anin da ya saukar mana. Mun yi imani da abin da aka saukar wa Annabi Ibrahim da 'ya'yansa, da Annabi Isma'il da Annabi Ishaq da Annabi Yaqub. Mun yi imani da abin da aka saukar wa Annabawan da suke cikin 'ya 'yan Annabi Yaqub. Mun yi imani da Attaura, wadda Allah ya ba wa Annabi Musa, da Injila wadda Allah ya ba wa Annabi Isa. Mun yi imani da littafan da aka ba wa Annabawa gaba xaya, bama bambance wani daga cikinsu, wato mu yi imani da wani sashe, mu bar wani sashe, a'a mun yi imani da su gaba xaya. Mun miqa wuya ga Allah, shi kaxai tsarki ya tabbata a gare shi. (137) Idan Yahudawa da Nasara da sauran kafirai sun yi imani irin wannan imanin naku, to sun shiriya zuwa ga tafarki madaidaici, wanda Allah ya yarda da shi. Idan kuwa suka bijire ga yin imani, suka qaryata da dukkan Annabawa, ko da wasunsu, to suna cikin savani da gaba da junansu. Kada ka yi baqin ciki – Ya kai wannan Annabi – Allah zai isar maka su, ya kare ka daga sharrinsu, ya taimake ka a kansu, domin shi yana jin maganganunsu, kuma ya san niyyoyinsu da ayyukansu. (138) Ku riqe addinin Allah wanda ya halicce ku a kan shi, zahiri da baxini. Babu wani addini da ya fi addinin Allah kyau, kuma shi ya dace da xabi'ar halittarku, yana kawo abubuwa masu kyau, yana hana munana, kuma ku ce, "Mu masu bautawa Allah ne, shi kaxai, ba ma haxa wani da shi". (139) Ka ce – Ya kai wannan Annabi –Yanzu ku ma'abota littafi kuna jayayya da mu, akan cewa ku ne kuke kan addini, kuma kuke da kusanci da Allah fiye da mu, saboda addininku ya fi daxewa, kuma littafinku ya riga namu sauka?. To ku sani hakan ba zai amfane ku ba. Allah shi ne Ubangijinmu gaba xaya, ba naku ba ne ku kaxai, muna da ayyukanmu waxanda ba za a tambaye ku a kansu ba, ku ma kuna da ayyukanku waxanda ba za tambaye mu a kansu ba. Kowa za a saka masa da ayyukansa, mu kuma masu tsarkake ibada ne da biyayya ga Allah, ba ma haxa kowa da shi. (140) Ko kuna cewa – Ya ku ma'abota littafi – Annabi Ibrahim da Annabi Isma'il da Annabi Ishaq da Annabi Yaqub da Annabawan daga suke cikin 'ya'yan Annabi Yaqub, suna kan addinin Yahudanci ko kiristanci ne? To ka ce da su – kana mai ba su amsa - Ya kai wannan Annabi: "Ku da Allah wa ya fi wani sani?!. Idan suna raya cewa waxannan Annabawan suna kan addininsu, to sun yi qarya, domin an aiko waxannan Annabawa, kuma sun mutu, tun kafin saukar da Attaura da Injila. Don haka abin da suka faxa qarya suke wa Allah da Manzanninsa, sun voye gaskiyar da aka saukar musu ne. Ba wanda ya fi zalunci kamar wanda ya voye shaidar da ya sani, kamar yadda ma'abota littafi suke yi, kuma Allah ba gafalalle ba ne daga ayyukanku, zai saka muku a kansu. (141) Wannan al'umma ce da ta wuce, ta tafi zuwa ga abin da ta gabatar, don haka tana da ladan abin da ta aikata, ku ma kuna da ladan abin da kuka aikata, ba za tambaye ku ayyukansu ba, su ma baza tambaye su akan ayyukanku ba, ba za a kama wani da zunubin wani ba, ba wanda zai amfanu da aikin waninsa, kowa za a saka masa da abin da ya gabatar.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Da'awar ma'abota cewa suna kan gaskiya baza ta amfane su ba, alhali sun kafirce wa abin da Allah ya saukar ga Annabinsa Muhammad (S.A.W). 2 - An kira addini da sunan "rini", saboda yadda ayyukansa da siffofinsa suke bayyana a jikin musulmi, kamar yadda rini yake bayyana a cikin tufafi. 3 - Yarda da Allah Maxaukakin Sarki shi ne Ubangiji da bautar masa abu ne da yake cikin xabi'ar bayin da Allah ya halitta. Shaixan ne da mataimakansa suke vatar da su daga barin hanyar gaskiya.**